KƙASAITA BOOK 3

NA

MARYAM KABIR MASHI

Page 1

Lafiyayyar dardumar kafet muka dinga takawa har izuwa wajen su waziri, waɗanda su ne iyayen fada. Ya ɗan sunkuya ya gaishe su, nima sai na yi yanda na ga ya yi. Madadin na ga sun amsa cikin nuna isa,su manya ne, sai na ji sun yi masa ɗan ƙaramin kirarin yabo.

Yana ɗagowa kuwa, sai na ga sun bi layin gaisawa da shi, wato ya dinga bin su ɗaya bayan ɗaya yana gaisawa da su. Ni kuwa da mun iso sai in ɗaga masu hannu. Suna gamawa dogarawan nan na zubewa ƙasa, domin gaishe da mu. Mamaki kam ya dirar masu a lokacin da suka bayyana shi a fili, shi ne amsa musu da ya yi da.

"Mun same ku lafiya?" Har da ɗan jan sunayen biyu daga cikin su. Ba su ba,ko ni nayi mugun mamaki.

Shi kuwa wucewa ya yi abinsa bai tsaya neman ba'asin mamakinsu ba, balle da ya ce su tashi mana. Me ye na saurin zubewar su ƙasa. Da ya isa ga wasu masu kayan mu na gida kuwa, ma'ana ta da ganinsu ka san ba dogarawa ba ne, ba wanda ko ni nasan na kusa da shi ne, ban dai san ko su waye su ba,abokanansa,ko ƴayƴan manyan fada. Yana isa ya rungume ɗaya daga cikinsu, kowa kam ya yi mamakin haka, ya dinga binsu ɗaya bayan ɗaya yana yi masu masabahar runguma, irin gaisuwar larabawa,su ma kuwa sun kai su taƙwas. Bayan nan kuwa muka juya motar mu wadda aka buɗe ta tun kafin mu isa gare ta.

Limousine ce, amma na san ba wacce na san Yarima da ita ba ce ba, saboda waccan baƙa ce mai ƙofa uku, kuma gabanta irin na kowacce mota ne, amma wannan ruwan toka ce mai duhu ash colour, sannan gabanta tamkar End of Discussion. Sai da na shiga sannan na ga ya zagaya shi ma ya shiga.

Subhanallahi!. Ba don kada a ce na ruɗe ba, da sai in ce motar nan ta fi jirgi daɗi da ƙyau, duk da na je ƙasashe na gano kala-kalar motoci da jiragen sama kansu.

Lulluɓe muke ta ko'ina, ba mai ganinmu. Na ja jiki na isa na ƙwanta kafaɗar mijina. Ya ɗago goshina kaɗan ya sumbace ni.

"Thank you. Au! Ɗan ɗaga ina zuwa, kada na yi laifi biyu." Ya ɗan ware ƙafafunsa, sai na ga ya janyo wani abu kamar ɣar sabuwar alkyabba mai ruwan hoda, ya dinga zarowa har da ɗan mayafinta, shi ma mai ruwan hoda.

Ban da takalma da jaka masu ruwan ƙasa,jakar wata ɣar maƙalalliya ce,a silin hannu kawai ake maƙala ta.

"Cire ta jikinki ki saka wannan. Gidan Mai Martaba za mu wuce mu gaishe shi,mu gaishe da Mama." Ya janyo ni ya ja hancina.

"Har wajen Daddy za mu fa yau." Ina zaro idanuwana.

"Me ye?"

"Ni kunyar shi nake ji." Na faɗa cikin shagwaɓa.

"Me yasa ki ke jin kunyar shi?"

Na ɗan harare shi irin hararar da na san zata sa idanuwana su yi mishi ƙyau. Ya yi dariya.

"Kin san kullum ina ƙara son ki da ɗokin ki Yasmin,saboda yanda ki ka mayar da ni autan ki."

"Na daina,ni dai kada a je wajen Dad."

"Ba zai yiwu ba,watan mu nawa da aure har yau ba ki taɓa zuwa gida ba. Ko a da da kika ga naƙi kai ki, tsoro nake ji kada in na kaiki ki ce ba ƙya dawowa. Ki sani na koma uku saura ƙwata a garin nan. Yanzu kuwa ko kin ce ma na san yanzu ina da garanti ɗin bin ki duk inda ki ka nufa, yanda suka ba ki ɗaki, nima haka za su ba ni,in ba haka ba ƙwanan falo ya kama ni. Ke ni ko kicin ma na dinga ƙwana,ai dai ina ganin ki kullum."

Na ɗan ture shi kaɗan tare da ɗan narkewa alamar shagwaɓar da na san tana sa shi ya ji daɗi. A take ya yi yar ƙara kaɗan.

"Ina! Ashe da nayi sakaci a baya da ƘASAITA ta janyo mini haɗarin da yafi na mota wahala. Rasa ki Yasmin ai wani babban gurguntar rayuwa ne."

"Ni?"

"To ya isa, na daina."

"Na ɗora saman kayan jikina,dama kuwa wani material ne mai ƙyan gaske (yadi), shi ma naga ya cire ta jikinsa ya saka fara tas. Dama kayan jikinsa boyal ne baƙi,safari da wando irin ɗinkin sarauta, sai ya ɗora ruwan tokar alkyabba yanzu ya tuɓe ta ya ɗora fara.

Na zaro foda mai tafi da madubinta, na ƙara gyara fuskata na ƙara rangaɗa ƙwalli wanda dama ni kaina na san na yi kalar ja, tamkar jini zai fito daga jikina. Na ƙara gyara gashin idanuwana suka miƙe tsaye, ban da baƙi da suka ƙara, juyowar da zan yi sai na ga Yarima ya rabga tagumi ya ƙura min idanuwansa, tamkar mutum-mutumi, saboda ko ƙiftawa ba ya yi.

Sai da na kai ga taɓa shi, sannan na ga ya yi irin murmushin nan mai nuna alamar daɗi, ya yi masa yawa, ya ɗauko turare ya fara yi min fesar nan tasa. Duk fesawa ɗaya tare da sumbata ɗaya, wuya, baya saman ƙirjina, zuwa bayan kunne, wanda a ƙarshe ya kan ajiye turaran ya rungume ni da jikinsa,ko ma ya ɗauke ni cak ya tafi da ni, inda zuciyarsa ta fi so.

Amma yanzu na yi saurin ɗago shi daga ɗan ƙaramin fita daga hayyacinsa da ya yi, idanuwansa a lumshe, na sa yatsuna biyar na wara su saman fuskarsa na shafa zuwa ƙasa.

"Honey, we are in the car, wake up."

Ya buɗe idanuwansa da suke a lumshe ya yi murmushi, tare da lakatar hancina.

"Ba ƙya ji."

Na yi murmushi haɗe da ɗan fari da idanuwana, ya zame jikinsa ya ƙwanta a cinyata.

"Har na ji na gaji."

"Aikin me ka yi? Kai da Allah ya gama haɗa maka daɗin duniya, sauran ka fa lahira da addu'ar mata ta gari, yaya na gari."

"Mata ma na samu, yayan ma ina sa ran matata zata iya yi mini tarbiyyar su da irin tata tarbiyyar mai ƙyau."

Tsayawar mota ita tasa ya yi wani saurin tashi zaune cikin sakan ɗin da bai fi rabi ba, tare da gyarawa yana saka gilashin fuskarsa. Ana buɗe ƙofar nan da nan na ga har ya rikiɗe ya tafi cikin jinin sarautar sa. Kafin na ƙarasa kallon ikon Allah har an buɗe mini nawa ɓangaren take na tunano irin tawa ƘASAITAR a baya. Na yi saurin juyewa ni ma.

Ina kunno kai wajen motar nan na ga taron mutanen da sai ka ce wani biki ake,ko gagarumin taro. Yana tsaye har sai da na zagayo sannan muka jera da shi cikin kunya da naji. Muna isa cikin fada aka wuce kai tsaye,fadar ma ta waje, ba ta cikin gida ba.

Allah Sarki. Gaskiya Sarki yana son Yarima,son da na rasa cikin mu uku nawaye ya fi ƙarfi. Mama ko Mai Martaba ko ni? Wannan tunanin ya faɗo mini ne a daidai lokacin da muka shiga fada na ga Sarki ya yi saurin miƙewa tsaye yana fara'ar da ta bayyana a filin fuskarsa. So da so ya haɗe,a take Yarima ya yi saurin isa yana murna, ya tsugunna a gaban mahaifinsa, tsugunnon girmamawa, Mai Martaba ya sunkuya tare da dafa kansa.

Fadawa suka ɗauki roƙon kirarinsu, "Nan Sarki ya amsa."

Mai martaba ya ɗago shi, madadin ya sake shi, sai kawai na ga ya rungume shi. Fada ta ɗauki ihun murna har da tafi. Ni kuwa wani irin daɗi ya saukar mini a lokaci ɗaya, saboda Yarima na ɗagowa sai ya nunawa Sarki ni. Ganin haka yasa na isa na yi saurin tsugunnawa a gabansa. Ya dafa kaina nima. Gaba ɗaya fadawa suka ɗauki maganarsu.

"Sarki na amsawa, Gimbiyar mata wacce ta isa, gaba sarauta baya mulki,so da ƙauna dole a yi miki shi."

Ina tsugunne Sarki ya koma ya zauna, sannan duk faɗar aka zauna har da shi Yarima, ya tsugunna kusa da ni. A nutsuwa Sarki ya fara magana, wanda yɑn jarida da yɑn ɗaukar hoto da na talabijin sun zagaye fadar.

"Na godewa Allah da ya kawo ni wannan ranar ta farin ciki, shi ne ranar da Yarima mai ci gaba da mulkin mutanena ya dawo lafiya tare da iyalansa. Allah yasa masu albarka ga auren su. Ya yi tafiya ta hutu tare da iyalansa ta tsayin watanni uku. Allah ya dawo mana da shi lafiya, Allah ya bashi ikon riƙe iyalinsa lafiya da kuma al'ummar garina.

Na gode da irin karancin ƙaunar da ku ka nuna mana,ni da iyalina gaba ɗaya, Allah ya saka, ya kuma kawo mana canjin rayuwar jin daɗi a nan gaba. Kuma buƙatar da iyalinshi suka buƙata a takardar da ta iso min daga hannun jakadiyarsu,an gama ta tun wata biyu da suka shige, daga yau kuma iyalinsa na da iko da yɑncin zartar da hukunci a kan kowa,ko da kuwa hukunci a kan abin da suke son yiwa mutanena ne. Yanda suke son tsarin bayin gidansu, da masu kulawa da su ya koma a hannunsu. Na gode ƙwarai da ba ni haɗin kai da ake a game da hukuncin da na yanke,ko na gindaya. Yanzu za su shiga ciki domin ganawa da jami'ar da suka daɗe ba su gani ba."

Daga haka Mai Martaba ya yi shiru,ko motsi ban ƙara ganin ya yi ba. Duk da kaina a sunkuye yake, ganin Yarima ya matsa kusa da kujerar mulkin Sarki, ya dafa kansa ya miƙe tsaye,ni ma shi yasa na matsa aka dafa nawa kan, na miƙe na bi mijina da yake tsaye dama yana jirana.

Cikin gida kuwa, kamar ranar walimar amare bakwai, saboda mata da suka yi yawa a gidan. Maroƙa mata kuwa, sai yi suke, amma Yarima ɗaga kai kawai ya yi ya kallesu, sai na ga duk sun zube ƙasa suna ƙwasar gaisuwa. Gaskiya al'amarin sarauta da akwai sha'awa, sai kuma yanzu na tabbatarwa kaina cewa ba su ne da kansu suke nuna ƘASAITA ba, musamman Allah ne ya saka musu ita a cikin jininsu.

Falon Hajiya Kilishi muka fara shiga,a inda na ga hakan ba ƙaramin daɗi ya yi mata ba. Har ƙasa muka sunkuya muka gaishe ta, cikin daɗi ta amsa, har da kamo ni da tayi ta rungume,wai ga ɗiyarta ta dawo. Cikin zolaya irin ta manya ta fara magana.

"Amma dai nan za ta ƙwana, saboda gajiya,ai dole ne ta ɗan samu hutu."

Shi dai Yarima sai dai kawai ya yi murmushi, "Baka ce komai ba?"

"Hajiya ai yarki ce,ga ta nan."

Amma fa ya kasa ɗago kansa. Hakan yasa ni kuma na ƙara zolayarsa.

"Dama kuwa Hajiya duk na gaji, ga zaman jirgi,Gara na huta yanzu,ko sati biyu na ɗan yi."

Ya ɗago ta gefen ido ya harare Ni, Hajiya tasa dariya.

"Daina hararar ta,ku tashi ku je tunda ka yi mini rowar ta."

Ya miƙe yana kiran, "Hajiya ba da ke nake ba, da ita nake,. Manya na magana tana saka musu baki."

Aka saka ɣar dariya, muka fito.

Manyan mata kenan, iyayen gidan Mai Martaba,su Mama. Zaune take kamar yanda muka samu Hajiya Kilishi, cikin sakan ɗaya suka yi gaisuwa duk suka fice ɗaya bayan ɗaya, suna fita ta taso ta rungume ni jikinta.

"Your are welcome my daughter."

"Nifa mama?" Ya faɗa cikin ɣar shagwaɓar da yake yi mini. Kamar dai yanda na ga ya yi mata farkon zuwana gidan.

"Ina ruwana da kai ni kuma, sai ka koma can wajen Hajiya."

"Kai shi kenan,kun haɗe mini kai. Ita ma Hajiya cewa ta yi ta samu yɔa."

"Sai ka koma wajen Mai Martaba,ƙila shi yana so."

"Kai Mama."

Muka ɗan yi dariya, sannan na ga ya zauna ƙasa yana gaishe ta. Hakan yasa ita ma ta zauna tare da ni a kusa da ita.

Yƙan nasihohi ta yi mana na mu zauna lafiya, kada ta kuskura ta ji wata matsala ta taso a tsakaninmu. Nan ta ce mini idan har na ga tana shirin tasowa na bugawa Hajiya Kilishi waya ko na nemi shawarar jakadiya. Nan take ta ba mu labarin cewa, bayan tafiyarmu an yɔanta bayin gidanmu, amma da sunan za su cigaba da aiki, amma a dinga biyansu albashi. Na gidana kuwa,an ce su nemo miji a yi masu aure, wacce mijinta ya bar ta ta cigaba da zuwa, wacce ya hana ta ta yi zaman auranta,ko yanzu haka ake ciki.

Yƙan gidan yari kuwa, Mai Martaba cewa ya yi sai kin dawo za'a sallame su, shi ne zasu bi layi a karanta miki laifin kowa, wanda ki ka ga ya dace ki sallame shi,ki sallame shi, wanda bai dace ba ki san ya zakiyi da shi. Na ji daɗi kuwa ƙwarai da gaske,a inda murnata ta ɗan fito fili.

A lokacin dai har Mai Martaba sai da muka ƙara keɓewa da shi na musamman, muka gaishe shi a fadar cikin gida. A lokacin ne ma na samu na yi godiyar abubuwan da ya yi mini, waɗanda na buƙata.

A nan shi ma ya yi mana nasihohi irin nasu na manya. Sannan ya ce Yarima ya yi taka tsantsan da rayuwa, saboda Abdulrahman ya zo da baya nan, har ya dinga rabon kuɗi a can gidan namu, ya ce a ɓangaren gidan Ahmad ya zauna. Sai da na ɗan nisa sosai, sannan na tunano wanda Sarki ke nufi, wanda Mama ta bani labari

cewa ɗan Sarki ne, amma baya sonsa, baya son ma a ce yʻayʻansa ne, kenan ɗan Hajiya Asabe.

Sai bayan da aka idar da sallar la'asar, sannan muka yi sallama da su. Ban tashi gane ina mota ta tsaya ba sai da aka buɗe mana ƙofa,kawai sai na ganni gidanmu. Na yi saurin kallon Yarima, sai na ga ya sha kunu, alamar babu wasa,ya ma yi gaba abinsa. Kafin ya kai ga yʻar matattakalar da ke ƙofar shiga gidanmu sai ga su Mamee sun fito, ita da Dad suna fara'ar murna.

Kunya ta yi saurin dirar mini,tare da murnar ganin iyayena da na yi, wata uku har da ƙwanaki da dama ban gansu ba, balle ma Dad ɗin da ba na iya ƙwana uku a da ban ganshi ba,ko tafiya ya yi saboda ni baya daɗewa, ya san har kuka nake yi masa a waya.

Yarima na isa na ga ya tsugunna ƙasa yana gaishe su. Shi kuwa Daddy sai naga ya ɗaga shi ya rungume, irin dai gaisuwar nan ta larabawa.

Dad cewa yake, "Oh! My Son, welcome back,I am happy to see you."

Ni kuwa ina isowa na faɗa jikin Mamee wacce kai tsaye tana dariyar murna. Ta ɗan riƙe ni tana dariya, daga baya kuma sai da ta taɓa ɗan wasan da ta saba.

######

[2/18, 09:13] Ummi Tandama😇: *ƘASAITA BOOK 3*

NA

MARYAM KABIR MASHI

"Ke tashi daga jikina,ko yʻata ba ta zo ta haye mini jiki ba sai ke."

"Kai!" Na faɗa cikin yanayin jin kunya da shagwaɓa."

"Ke zo nan ƙyale ta dama ita haka take."

Cikin jin kunya, na isa wajen Daddy, Amma sai ga ni na tsugunne a ƙasa, saboda kunya da ta kama ni. Ya sunkuyo ya ɗago ni ya rungume a jikinsa. Kʻamshin turaren sa na ji ya dakar mini hanci. A take na ji kaina ya sara. Cikin sakan ɗaya na ji ina juyawa tamkar wacce ta yi hajijiya ta gaji (Katantanwa), wani amai na ji mai zafin gaske yana taho mini. Tun ina ɗaurewa har na ji gashi nan ya gangaro a bakina. Na zame jikina daga rungumar da Dad ya yi mini,na ruga a guje ga famfon da ake bawa fulawowi ruwa, na tsugunna. Wani irin mugun amai na dinga ƙwaranyawa. Ni dai na ji an riƙe ni, amma ban iya ɗaga kai ba ballantana in ga waye mariƙin nawa.

Tun ina yi daga tsugunne,sai ga ni na durƙushe sosai, shi kuwa aman nan ya ƙi tsayawa ko shan iska ma in yi. Na ƙwashe tsayin minti goma ina ƙwaranya amai. Sai ya yi kamar zai tsaya, sai kuma in ji wani sabo ya taso. Muryoyin sannu kuwa,ta ko'ina a kunnuwana, mai dafani kuwa, sai na ji ya tsugunna ya rungume ni a jikinsa.

Jin aman ya tsaya, yasa na samu na miƙe na isa na buɗe famfon na kuskure bakina, tare da wanke fuskata, saboda hawayen aman da suka tsattsafo ga idanuwan nawa. Sai da na juyo na ga mutane tsaye a kaina kusan mutum goma sha,yʻan aiki, masu gadi.

Mamee ce rungume da ni. Dad kuwa yana tsaye yana kallon ikon Allah, dukkansu suka yi mini sannu. Daga nan Mamee na ɗan riƙe da ni har cikin falon Dad ɗina. Na

ɗan kishingiɗa kaɗan a kujera,Dad ke tambayata me ya ke yi mini ciwo? Na ce ba komai, sai dai kaina kawai. Cikin rawar jiki Daddy ya ɗauko magani ya miƙa mini. Mamee ta karɓa.

"A'a ba a shan magani ko sai an ga likita. Ka bari in sun tafi can su ga likita, sai ya rubuta musu magani."

Nan take na ji Dad ya fara faɗa, "Ya ma za'ayi a ce sai ta ga wani Likita,ai kowa ya san maganin ciwon kai."

"Ka zo ciki Alhaji." Ta yi ciki. Na san ɗakin Daddy suka nufa. Nan fa Yarima da ke zaune gefe ɗaya ya yi ɗan ƙaramin zaman makokin cutata, ya samu damar saurin isowa gare ni, ya kama ni ya rungume ni da rawar jikinsa.

"Ya ya me ke miki ciwo? Ki gaya mini kin ji Yasmin, talk to me please."

"Bana jin komai, sai dai kaina da ya yi mini nauyi kamar yana ciwo."

Ya sake ni ya durƙusa a gabana, ya rike hannayena duk biyun, "Please Yasmin, tell me the truth."

"Ba komai,ni bana jin komai."

"Yasmin look at me." Na ɗago na kalleshi.

"Kada ki ɓoye mini Yasmin,ki kalleni ki ga yanda na koma a yanzu kawai. Kina tunanin in ki ka ɓoye mini ya zan koma a nan gaba?"

Ya sumbaci hannuwana. Na zame hannu ɗaya na shafi gefen fuskarsa, tare da sunkuyowa na sumbaci laɓɓansa cikin kunya.

"Ba zan taɓa yi wa mijina ƙarya ba saboda ina son shi ba zan so in ga hankalinshi ya tashi ba. Ka amince da abin..."

Motsin da muka ji yasa ya yi saurin tashi ya koma inda yake zaune. Shi ne kujerar da ke nesa da ni.

Dad ne ya shigo, amma sai na ga damuwar fuskarsa ta gushe, wanda take kaɗan ya yin da Mamee ta biyo bayansa. A nan Mamee ta ce mu shiga ciki mu bar su nan. Na miƙe tare da satar kallon Yarima, saboda in karanto me ke fuskarsa. Cikin maganar raɗa ya ce, "Take care." Na lumshe ido alamar na amsa masa na wuce cikin gida.

Mamee ta zaunar da ni ta dinga yi mini yʏan tambayoyi kamar su, "Ba komai dai zaman ki da mijinki? Ya ya yanzu kun daidaita ko? Ya gida? Sarautar ba dai matsala?"

Duk na amsa mata da eh kawai. Saboda na san ni yanzu ba ni da wata matsala dama matsalata ɗaya ita ce Yarima, yanzu kuwa ni kaina na san ina son Yarima. To ballantana shi wanda na lura da zai iya rasa rayuwarsa idan har ya rasa ni.

Sai ƙarfe uku muka bar gidan, amma kafin in tafi tamkar ban taɓa yin komai ba, saboda sai da ma na ci abincin Mamee na ƙoshi. Lafiyata ƙalau muka yi sallama da su. Duk da sai da na nunawa Yarima ya bar ni gida tsayin ƙwana baƙwai,a lokacin muna falon Mamee. Wannan ne ma ya baiwa Yarima damar cije mini laɓɓana da harshensa kada ma na sake faɗar irin wannan mummunar maganar. Na ɗan narke masa tare da cewa.

"Gidan mu ne fa! Yanzu shi ne mummunar maganar?"

Bai ma ba ni amsa ba, sai dai ya ɗan kama hancina ya ja ya tafi falon Daddy,wato manufarsa baya son maganar ma.

Muna shiga mota na ƙwanta daidai lokon motar.

"I am tied." Har da ɗan canja yanayin fuskata. Bai fi minti ɗaya ba na ji Yarima na kiran sunana. Na juya na kalleshi, sai na ga ya ware hannuwansa, alamar in isa gare shi. Na ɗan kaɗa idanuwana na gyara ƙwanciyata sosai, alamar dai ba na zuwa.

"Honey please come on. Ina son jin ɗumin jikinki a kusa da ni."

Na matso na faɗa ƙirjinsa na ƙwanta tamkar ba ni ba, ina jin shi ya sumbaci goshina. "I love You Yasmin,I can't explain how much I love you. Amma ke kina ɓoye mini me ke cikin zuciyarki.

Yasmin kin san ba zan iya yin komai ba sai kina kusa da ni. Me yasa za ki takura mini in bar ki gida? Wallahi ba zan iya ba,in ba so ki ke inyi ƙwanan ƙofar gidanku ba, amma na lura ranki ya ɓaci don na hana ki. Yasmin ki yi tunani, ba ki da lafiya fa, ya zan iya ƙwatanta ƙwanan da zan yi a yau in na tuna haka?"

Jin maganganun za su yi yawa na san halin Yarima, yanzu zai iya shiga matsananciyar damuwa idan na yi masa shiru. Na ɗago nasa tsinin hancina a daidai bakinsa.

"Ka yi haƙuri ba zan ƙara ba. Wallahi nafi son ganin farin cikin ka fiye da nawa. Na fi kowa baƙin ciki idan na ga kana cikin shi. Ka yi mini afuwa,ɓata maka ran da na yi ba zan ƙara maimaitawa ba...."

Ya ɗago ni, "kin ci abinci?" Na ɗaga masa kai.

"Are You sure?" Na ɗaga kaina.

"Ai na yi wa likita waya, har ma na gayawa Mama na ce ta shaidawa Mai Martaba cewa ba ki lafiya za mu koma gobe."

"What? Haba Yarima, daga ɗan amai kuma sai ka damu haka."

Na sassauta murya, "Ka yi ƙoƙarin ɓoye sona a zuciyarka,fitowa da shi fili zai iya janyowa mutane su tsane ni."

Ya ɗago ni sosai, "Su tsane ki,su waye mutanen? Wa ya fara canja maki fuska? Gaya mini,kina so in sa duk a kashe su?" Na yi saurin rufe bakinsa cikin tashin hankali, kamar yanda na ga har ya rikiɗe mini ya koma Yariman farko.

Na yi sauri na sulale ƙasan mota tare da riƙe hannuwansa.

"Za ka yarda da duk abin da na faɗa?"

Ya ɗaga kansa.

"Wallahi ba wanda ya taɓa canja mini fuska, kowa na sona kamar yadda ka ke sona. Ina son cewa da kai ka rinƙa ɓoye na ka ne ka bar ni in dinga fito da nawa a fili."

Sai naga yayi ajiyar zuciya, amma kuma ya kasa magana, sai da ya ɗago ni ya rungume gam, tsayin minti biyu, sai na ji yana magana cikin sanyin murya.

"Yasmin ba ki san yanda nake jin ki ba a zuciyata. Kin ɗauka wasa nake ko?"

"A'a na san..."

Ta yi daidai da buɗe motar da aka yi, ya yi sauri ya rufe cikin ƙiftawar ido, jikinsa kuwa tun a lokacin ya kama rawa. Na gyara sannan na ji ya ɗan ƙwanƙwasa gilashin motar, cikin gaggawa aka buɗe mana ta ɗaya ɓangaren, na fito, shi kuwa ta

ɓangaren da yake. Sai a lokacin na fahimci gidan Aunty muka zo,gudun kada in ruga in baiwa kaina kunya da uban gidana yasa na tsaya tafiyar wahainiyar da muke ni da Yarima.

Falo kawai muka isa na dinga kwala mata kira. A firgice ta fito daga ɗaki, na ƙarasa da saurin guduna na rungume ta. Ita kuwa sai dariya take yi,tana cewa in sake ta taryi baƙon ta.

Mun samu sama da mintuna ashirin a gidan Aunty Salwa,sannan muka yi sallama da ita, wanda har alƙawari ya yi mini a gabanta zai kawo ni in yini in mun huta. Na dinga murna. Ganin jikin Yarima a sanyaye yasa har na fara shiga damuwa, na matsa na kama hannunsa tare da durƙusawa a ƙasan mota.

"Honey,me ye ya tayar maka da hankali? Wa ye kuma? Nima fa zaka jefa ni cikin damuwa?"

Ya ɗago ni ya zaunar da ni a saman cinyoyinsa, sai da ya sumbaci laɓɓana, sannan ya cire gilashin fuskarsa.

"Ke ce Yasmin, hankalina ya tashi matuƙa a kan ba ki da lafiya, amma ki ka ƙi gaya mini. Yanzu me iyayen ki zasu ce? Bana kulawa da ke?"

"Wallahi ni kaina ban san dalilin yin amaina ba,ni dai na san lafiyata ƙalau. Ni dai zan iya cewa ƙamshin turaren Daddy ne ya saka ni amai, kuma yanzu ni lafiyata ƙalau, zan iya yin komai, zan iya cin komai."

Na koma na ƙwanta a ƙirjinsa, "Kada ka ƙara damun kanka a kaina."

Sai na ga ya ɗago ni ko kasa me zai yi mini ya yi, sai kawai na ga ya dungure mini goshina.

"Kada ki ƙara faɗa mini haka."

A take ma sai na ji ya ba ni dariya. Na sa dariya irin ta nutsuwa, ya rungume ni, shi ma ya yi tasa dariyar irin ta su ta mulki.

A hankali na ga gilashin motar mu na sauka, wannan yasa na yi saurin sauka daga cinyar mijina na gyara zamana sosai. Subhanallah! Jama'a ne tamkar su ɓall gidanmu, tun daga get ɗin gidajen har izuwa harabar gidan mu. Jinjina ake yi, gaisuwa, amma yau Yarima ya burge ni, saboda ɗaga masu hannu da yake yi har da murmushinsa, mutumin da ba ya ko motsi idan ya shiga motar nan, to balle ma an canja wata motar wacce za ta iya ƙara masa girman kai, amma abin mamaki yau har da murmushinsa.

Motar mu na tsayawa na hango wani mutum a tsaye,shi kam tamkar wani saboda yanda na ga an zagaye shi. Sakan ɗaya da tsayawarta aka buɗe mana,kirari irin wanda ake wa Sarakuna, shi aka dinga yi wa Yarima. Gaisuwa da sauran hidimomi irin na sarakuna.

Wani abin da ya fi burgeni, shi ne wannan mutumin da ke tsaye tsakiyar nasa dogarawan, shi na ga an yi saurin kawo aƙwatin kuɗi a gabansa, aka buɗe masa irin na matafiya,brief case. Yana ɗaukar bandir sai dai ya ɓalle yʼar takardar ya watsa su. Amma mutanen mu ko matsawa ba su yi ba, ballantana su san ana zuba kuɗi a gabansu. Sai dai ma dogari ɗaya da yake gabanmu yana share su gefe,gudun kada mu taka. Wannan kuma ina jin dokar Yarima ce,sai ma a lokacin na lura cewa yʼan ɗari bibbiyu ne ake wa wannan watsin da su.

A nan na saki da sha'anin Yarima, wato har dogarawansa ma ya san yanda yake tafiyar da su. Wani abin mamaki Yarima bai tsaya wajen mutumin nan ba, ya yi wucewarsa, sai me? Ai tun daga barandar gidana na ga gidana ya canja. Yʼan matan gidana kuwa, duk sun taru a barandar, suna hango ni sai murna. Ni kaina duk sai na ji na ƙara ƙaunarsu. Mansura kuwa har da gudunta, ta iso ta durƙusa gabana ta kama hannuna. Na yi murmushi na ɗago ta, sai tasa kuka. Na yi murmushi na kama hannunta muka tafi.

#####

[2/19, 22:29] Ummi Tandama😇: *ƘASAITA BOOK 3*

NA

MARYAM KABIR MASHI

Page 3

Lallai Yarima " Na faɗa a zuciyata,ganin duk ya ɓyale mutanen da ke bin bayansa ya biyo ni gidana. Sai dai na ga ya yi wa wani dogari nuni da hannunsa. A take na ji dogarin na cewa.

"Yarima ya ce a jira shi ya huta. Yarima na gaishe ku. Nan da awa biyu zai fito."

Me zai faru? Ina kunna kai a gidana, na ji wani ɓamshin turaren wuta na tashi. Nan take kaina ya fara juyawa. Cikin ɗan sauri-sauri muka gaisa da jakadiya da jama'arta. Haka shi ma Yarima na ga yana gaisawa da su. Ko lura ya yi,ai muna hawa sama a guje na ɓarasa banɗaki. Yarima na bina shi ma tun kafin in kai ɗan wajen alwala,bath amai ya kubce mini. Alkyabbar jikina kuwa sai dai wata.

Yarima riɓe da ni na dinga ɓwaranya amai kamar dai yanda na yi a gidanmu. Nan take na ji Yarima na waya cikin mutanen shi na ji ya yi wa ɗaya magana. Wai ina likitan da ya ce ya zo gida ya jira shi?

Nan take na ji yana cewa,nan da minti biyar ya hayo sama da sauri yana son ganinsa. Ni kuwa har amai ya kai sai dai ruwa-ruwa, saboda abincin ya ɓare.

Ina gamawa Yarima ya kama ni wanda jikinsa har rawa yake, ya cire mini alkyabbar jikina, ya wanke min fuska. Ban da sannu da yake yi mini, ya ɗago ni idanuwansa sun yi ja, ban da hawayen da suka cika su, ya dinga shafar fuskata. Lallai na amince Yarima son gaskiya ne a jikinsa, saboda ya rasa me zai ce mini. Ya kama ni muka fito ɗakina, ina fitowa wani sabon aman ya taso. Na koma ciki da guduna. Ya biyoni ya yi tsaye a kaina, ina ta faman yunƙurin aman da ba komai a cikina.

"Mama Yasmin zata mutu ta bar ni. Ki zo Mama."

Wannan maganar da ya yi ita ta tabbatar min waya ce ya yi, duk da ban iya ɗaga kaina na kalleshi ba.

"Ka hawo kawai." Wannan ya tabbatar mini da likita yake. Da sauri na ga ya fita, sai na ji yana cewa, "Shigo nan ka ganta. Sau uku kenan tana yin shi a yau,kaga har ya zamanto ba komai a cikinta, kalli yanda take?"

Likita ya sunkuyo, "Sannu Madam." Na ɗaga kaina kawai."

"Me ke saka ki amai?"

Na ɗaga masa hannu alamar ya jira, suna tsaye,Yarima na ta safa da marwa a banɗaki. Har tsayin mintuna goma, sannan na ɗago, wanda a take na ji jikina na rawar zazzaɓi. Ban da jiri da nake gani.

Yarima ya riƙe ni muka fito ɗaki. Muna fitowa na yi saurin komawa banɗaki.

"Yarima bana son warin turaren wutar nan, kaina juyawa yake yi."

Nan da nan ya kuma ruɗewa, "Doctor, ya za'ayi?"

"Yallaɓai ko a tafi da ita sashenka mu gani."

"Haka za'ayi."

Da sauri na ga ya buɗe ƙofar, bayan wacce za'a fita barandar baya, wacce ke kallon ta gidan Yarima, sai da ya buɗe, sannan ya kamo ni. Muna fita madadin in ga fili kamar da, sai na ga an gine ta, ta yi wani zagaye kamar ƙaton fayif na ruwa, ga fulawoyi na gaske nannaɗe da jikinsa.

Ban iya tsayawa na lura da yanda aka yi ta ba sosai, ni dai na ga muna tafiya har mun ɓulla ƙofar barandar Yarima. A take na ga ya buɗe mun shiga, sai na ga ɗakin Yarima. Yana isa ya ƙwantar da ni a gadon shi, ya janyo bargo ya lulluɓa mini,sannan ya koma ga kaina ya zauna, inda likita ya matso ya tsugunna gabana.

"Madam kamar me ki ke ji yana yi miki ciwo.?"

"Zazzaɓi, ciwon kai, sai amai."

"Mara fa,ko ciki?"

"A'a."

"Yanzu za ki iya tuna ko ƙwana nawa rabon ki da al'ada?"

"Likita bana son irin waɗannan tambayoyin fa." In ji Yarima.

"To Yallaɓai an bar su, sai dai ina son fitsarinta, yanzu zan je in dawo. Awa ɗaya za ka bani."

"To ya za'ayi a ɗebi fitsarinta,in ba ya ga rashin hankali irin naka?"

"Allah ya ja da rai,ga yɔar ƙwalbar da za ta yi a ciki ta bani. Yanzu zan tafi da shi, zan yi wani ɗan aiki ne da shi. Wannan kuma jininta za'a ɗiba.

Ya fito da sirinjin ɗaga aƙwatin hannunsa, sannan ya ɗauko wani abu yasa a kunnanshi, sai na ga ya ɗaure mini hannu da wani abu kamar balt (belt).

"Ba hawan jini, Yallaɓai,a taimaka a bayar da jinin da fitsarin." Ya janyo sirinjin zai ɗauki jini. Yana sa allurar na ɗan yi yɔar ƙara.

"Ka bi a hankali fa,in har da ciwo ka barshi kawai."

"Ai an ɗauka ma, sannu." Ya kama ni ya kai ni banɗaki, sai da muka isa ya tsayar da ni, ya tallabe kumatuna, ya dinga shafa su. Da gani ya rasa me zai ce sai kawai na ga ya haɗa bakina da nasa yana tsotsa, ya sake ni.

"Ya zan yi Yasmin?"

"Bana jin ciwon fa."

"Ga jikinki nan da zafi, ga shi har jikinki ya yi laushi." Ya sake ni ya fito kawa.

"Ina fitowa da yɔar ƙwalbar fitsarin a hannuna ya yi sauri ya tarye ni ya karba.

"Tashi likita." Ya kalli agogon hannunsa, ƙarfe huɗu da rabi.

"Nan da biyar da ashirin ina son in ganka cikin gidan nan."

Da rawar jiki likita ya karɓa ya tafi yana cewa, "Insha Allahu Yallaɓai, alheri ne."

Ni ke ƙwance, lulluɓe da bargo, shi kuwa tsugunne a bakin gado, yana ta faman shafa mini fuskata da bayan hannunsa, na mayar da idanuwana na lumshe, sai na ji yana cewa.

"Yasmin." Da sauri na buɗe ido, sai na ga ya yi ajiyar zuciya.

"How do you fell?

"Da sauƙi."

Ana haka Mama ta shigo har da Hajiya Kilishi da wasu su uku. Ya yi saurin taryarsu.

"Mama ga ta nan,zo taɓa jikinta ki ji."

"To mu je." Suka iso gabana.

"Yasmin ya ya jikin?"

"Taɓa jikinta ki ji Mama."

"Na gani ma ba sai an taɓa ba, likita ya zo?"

"Yanzu ya tafi, amma yanzu zai dawo."

"To shi kenan, bari mu jira dawowarsa, sannu Yasmin."

Na ɗaga kai, dukkansu ma suka yi mini sannu, sannan na ji Mama ta ce bari su zauna a nan falo, shi kuwa cewa yake.

"Mama kada ku tafi fa, Mama mutuwa za tayi?.

"A'a."

"Za ta tashi."

"Eh." Ta juya suka tafi. Ko awa ɗaya ba a cika ba, sai ga likita ɗauke da wata ƴar talabijin ɗin ƙwamfuta da shi da wani ɗauke da wasu tarkace a hannunsa. Ya shigo, ya gama jonawa cikin mintunan daba su wuce biyar ba, sannan ya iso wajen Yarima da yake tsaye a kaina." Yallaɓai muna son za mu ɗauko hoton marar ta kawai."

"Bismillah."

"Tsaya ina zuwa." Ya iso ya janye rigata a hankali, tare da rigar ciki ta shimi. Cikin ƴan mintuna ya ce ya gama.

"Me ye."

"Bari mu yi magana da Hajiya, tana falo."

Ya juya ya fita. Cikin mintuna biyar ya leƙo ya ce zai tafi,yana fita su Mama suka shigo.

"Yasmin mu mun tafi, Allah ya bayar da lafiya."

"Mama me ye wai.? Me likita ya ce muku?"

Ko nima sai na ji gabana na faɗuwa da sauri da sauri,cutar me gare ni kuma? Na tambayi kaina. Tambayar da Yarima ya ƙara yi wa Mama ita ta mayar da hankalina gare su.

"Mama don Allah ki gaya mini?"

"Wai me yasa baka tambayar Hajiya ga ta nan sai ni da ka raina? Ku mu je ku ƙyale su." Suka yi gaba abinsu, sai ya bi Hajiya.

"Hajiya me ye?" Sai da ta kusa isa ƙofar fita, sai na ga ta tsaya. Bana jin abin da suke faɗa, amma ni tuni har gefen filona ya jiƙe da hawaye, balle yanda na ji amsar da Mama ta bayar.

Ina kallon su shi da Hajiya, sai na ga ya dafe ƙirji duk hannu biyun,can kuma na ga ya durƙusa ƙasa da gwiwoyinsa duk biyu.

Amma sai na ga yana dariya, ya ɗaga hannu sama, ita ma Hajiya ta yi waje tana dariya. Tana fita, na ga ya rugo a guje ya faɗa saman gadon, cewa yake.

"Allah kana ƙaunata, da za ka ƙara mayar da Yasmin ta zama tawa har abada."

Ya wuntsulo ƙasa ya tsugunna, sai na ga ya janye bargon jikina, ya ɗaga cikina ya shafa fatar shi, ya sunkuya ya sumbace shi. Ya ɗago ga fuskata, ya goge hawayen da yake ta ƙwarara a gare ta.

"Yasmin na rasa da wane baki zan yi miki godiya."

Ya sumbaci goshina, ya dawo ya shafa cikina.

"Yasmin abin farin ciki ya same mu ya ya zan yi miki bayanin shi?"

Ya ɗago ya ƙura mini idanuwan nan nasa masu firgita ƙaramin yaro. Ya ɗago cikina sosai ya rungume shi, tare da ƙwantawa a saman sa.

Ya ɗago, "Baby na ne a nan Yasmin. Na zama Daddy daga yau, kada ki ƙara kira na da Yarima, sai dai Baban Yarima." Ya kanga kunnensa.

"Lah! Yasmin,kin ji wai yɗan biyu ne."

Nan take na gano me yake nufi. Kunya ta yi saurin dirar mini. A take na tambayi kaina, kenan ciki gare ni? To ni ya zan cewa Daddyna,in ya ganni da ciki?.

Ya matso ya ƙwantar da fuskarsa a tawa,na rufe fuskata, ya yi murmushi ya sumbaci kumatuna, tare da faɗar.

"I'm proud of you." Ma'ana "ina alfahari da ke."

Sannan na ji ya miƙe tsaye, ina kallonsa ta tsakankanin ƙofar yatsuna ya fita daga ɗakin. Tsayin mintuna biyu ya yi, sai ga shi ɗauke da ɗan faranti a hannunsa, ya zauna bakin gado tare da ajiye farantin da tree top ya ɗago ni, sai da ya matsa mini na sha, sannan ya ba ni magani ƙwaya ɗaya na sha, na koma na ƙwanta.

Ƙwanciyata ta yi daidai da wata ƙara mai ƙarfin gaske kamar ƙarar bindiga. Ban da ihu da muka ji mutane na yi. Ba Yarima da ke zaune ba,ko ni dake ƙwance ina fama da zazzaɓi, sai da na miƙe cikin sauri. Gaba ɗayanmu sai ga mu tsaye jikin taga, ban da ƙura da ta turnuƙe wajen.

Bayan kamar mintuna uku, sai muka ga ƙura na washewa a hankali. Ganin wani mutum muka yi a tsaye zagaye da shi, ana ta watsa kuɗi, jama'a na ta tsinta. Yarima ya juyo ya kamani.

"Zo ki ƙwanta, bari na sauka ƙasa na dawo."

"Ka turo mini jakadiya." Ya amsa da to. Ya yi waje.

Cikin mintuna sha biyar sai ga jakadiya a nan nake tambayar ta me ke faruwa? Bayan gaisuwar da ta yi mini,a nan take ba ni labari wai wani ɗan Sarki ne ya zo, tun ba mu daɗe da tafiya ba. Ba yaudarar da ba ya yi a gidan nan, shi ne rabon kuɗi, abinci da sauran kayayyaki, duk wanda aka kaiwa ya ƙi karɓa, to zai faɗa ne. Take gaya mini ko ita an bata magani ta zubawa Yarima a abinci da sauran wurare.

"Kin karɓa?"

"Eh, saboda in ka ƙi karɓa sai dai a wayi gari ba kai."

"Ɗan Sarkin wane gari ne?"

"An ce babban Yayan su Yarima ne,wai shi Abdulrahman."

Na yi shiru. A nan take na tunano labarin da Mama ta ba ni, ina cikin wannan tunani sai ga Yarima ya shigo da saurin shi.

"An kashe mutum uku a wajen can."

"Me ye dalilin kashe su?"

"Wai saboda sun ƙi ɗibar kuɗin da yake sa wa ana watsawa."

"Wa ye shi?"

Wai Yayan mu ne."

"Meye dalilinsa na yin haka?"

"Sarauta yake so."

Na yi shiru tare da faɗuwar gaba mai tsanani saboda tunanin kada a kashe mini mijina.

Canja alkyabbar jikinsa ya yi, ya ƙara sa turare a jikinsa.

"Ina za ka?"

"Wa je." Na miƙe da sauri.

"A'a kada ka fita ya harbe ka."

Ya yi murmushi.

"Ai mu ba'a kashe mu ta nan ɓangaren."

Ya nuna jakadiya da ɗan yatsa.

"Kin ga wacce za ki danƙawa amanar mijinki nan. Sai kuwa masu dafa mini abinci, ta sanadiyyar su ake yi mini komai."

Ya iso inda nake tsaye, ya tallafi kumatuna, cikin nutsuwa ya fara magana.

Kada ki tayar da hankalinki,ki yi tunanin cewa kina da yaron ciki, zai iya zuɓewa ta kowanne hali,ki ƙwantar da hankalinki."

Hawaye suka ƙarasa gangarowa.

"Ni dai ban yarda ba."

Ya yi murmushi, "Yasmin kada ki karaya mana. Ki tuna gidan sarauta fa ki ke. Haba Honey."

Na ƙwantar da kaina a ƙirjinsa, sai kuka sosai. Ya ɗago ni ya ƙura mini ido ba tare da ya yi magana ba. Ɗan tsayin minti ɗaya, sai kawai na ga ya mayar da ni ya rungume ni sosai. Ya ɗago ni da saurinsa ya sumbaci goshina, ya dawo ya tsotsi bakina,bai ce komai ba ya ɗauke ni cak ya ɗora a gado. Ya ja bargo ya lulluɓe ni, ya sunkuyo yana gyara gashin kaina, wanda ya zubo a fuskata,ko in ce wanda ya hautsine saboda ƙwanciya.

#######

[2/20, 13:07] Ummi Tandama😇: *ƘASAITA BOOK 3*

NA

Ya ƙara sumbatar goshina, kawai ya juya ya tafi. Bin shi na yi da kallo, shi yasa idanuwana suka gane mini ba jakadiya a ɗakin nawa. Yana fita tana shigowa na mayar da kaina na ƙwantar,sai na ji hawaye sun ƙi tsayawa. Jakadiya ta iso ta tsugunna gaban gadona.

Allah ya ja da rai,ai ke ce ya kamata a ce kin ƙara ƙarfafa masa gwiwa tare da shawarwari, ke ce mace,kin fi shi tausayi, ke ya kamata a ce kin tsaya kin lura da tambayar me yakamata a yi wa talakawa,shin hukuncin da bai cancanta ba a yi shi?"

Na tashi zaune. "To yanzu jakadiya,kina jin ya ce an kashe mutum uku, wacce kuma daraja gare shi,ai kin ga bai dace ba ya fita, sai ya tsaya ya ga ya zata kasance."

Ta yi murmushi, "Yana shugaba? Ai shugaba bai ga ta zama ba, ke dai kiyi ƙoƙari ki koyi dabarun taimakawa mijinki da shawarwarin da zai sa jama'arsa ta bi shi, ta kuma ƙara ƙaunarsa."

"Kin san su ne ke? Saboda ni kin ga ba yɑr sarauta ba ce ba,haye min tayi da rana tsakiya. Kin ga kuwa ba zan san komai ba game da ita."

Jakadiya ta yi murmushi, ta ƙara gyara zama. Tun da ta fara magana nake tallaɓe da kumatuna, saboda al'ajabin abubuwan da take faɗa. Wannan ne yasa a take na ɗauki waya na daddana, domin neman Yarima, saboda fara gudanar da dabarar ta farko cikin dabarun da jakadiya ta koyar da ni. Amma ina! Hayaniya ta yi yawa,ko ƙarar ta ma ba ya ji. Wannan yasa na yi haƙuri sai ya dawo gida, na umarci jakadiya

da ta je tasa a sa fanka a kori duk warin turaren da suka saka a gidana. Na bata room Freshner gidan Yarima na ce a sa mini ita.

Yariman bai samu shigowa ba sai ƙarfe tara da rabi na dare. Cikin nutsuwa ya zo ya zauna gefen gadon da nake ƙwance, ya sunkuyo ya sumbaci laɓɓana.

"Sannu da dawowa."

"Ke zan yi wa sannu, ke da na barki ba lafiya, na so shigowa in ga jikinki,amma ina, na so in gaishe ki ko da a waya ne, amma duk hakan ba ta samu ba, sai yanzu ma na ga kiran ki a wayata, missed call,ki yi haƙuri ban ji ba."

"Ba komai. Yaya komai dai ya tafi lafiya?"

"Eh, to hakan nake tsammani."

"Wai me ye ya faru?"

"Wani mutum ne ke neman tayar mana da fitina, shi ne na sa aka kama shi har da yaransa, wajen goma, bayan an kama su ne na turawa Mai Martaba Sarki da aiken cewa ga masu son tayar da zaune tsaye an kama. Kafin Mai Martaba ya iso shi ne nasa aka tara jama'a na basu haƙuri da dai bayanan da zai kwantar masu da hankali." Ya koma ya ƙwanta rigingine,saman jikina.

"Kin san ko waye mai son haɗa mana rigimar nan?"

Na ce "A'a." Cikin sanyin murya.

"Wanda na gaya miki ne wai shi Abdulrahman,wai ɗa ne ga Mai Martaba, amma baya son ma a na faɗa, saboda ko a yanzu ma bai bayyana ba,ba kowane ya ji ba. Ni ma waziri ne ke gaya mini."

Ya yi ɗan shiru. "Dama ni Mama ta taɓa ba ni labari cewa akwai su,su biyu ne ma har da Yayarsa. Yanzu dai Mai Martaba ya ja masa kunnansa cewa idan ya ƙara jin labarin ya zo garin nan sai yasa an kashe shi."

Na shafa gashin kansa, "Ka ƙwantar da hankalinka, ba ka tambaye shi cewa me yake so ba.?"

"Sarauta." Na ɗan yi saurin alamun tashi haɗe da tambayar.

"Sarauta ta me?"

"Ta Mai Martaba."

"To kai fa?" Ya yi murmushi, "kina son sarauta ne? Aƙwai wahala fa." Na ɓata fuska sosai.

Ya ƙara yin murmushi, "Yasmin kenan,ki ƙwantar da hankalinki,komai ya wuce, ina nan a matsayina na Yarima mai jiran gado, har da Babyna."

Ya faɗa yana lakatar mini hanci. Kunya ta kama ni. Na yi saurin tura kaina filo, shi kuwa ya kama yar dariya irin tasu ta sarakuna. Ya turo kansa cikin filon.

"Yauwa." Na yi saurin fito da kaina daga ƙarƙashin filon na yi alamar tashi da saurina.

Ya yi saurin mayar da ni ya zaunar, tare da riƙe min kunne.

"Kin manta ne ki ke tashi da sauri haka?" Ya ɗaga rigata ya sunkuya ya sumbaci fatar cikina, ya ɗago ya tallabi kumatuna tare da ƙura mini ido.

"Yasmin! Yasmin!!" Ya girgiza kansa.

"Ba zan taɓa iya ƙwatanta yanda nake jin ki ba a raina,son da nake miki yafi ƙarfin duk wani ƙaramin misali."

Na rausayar da idanuwana, waɗanda na ji sun aiko da hawaye. Mayar da su ɗin da na yi na runtse ya yi daidai da gangarowar su saman kumatuna,ni kaina ban san dalilin zubowar su ba, sai dai na ji zuciyata ta yi mini sakayau, ba nauyi. Na san ba abin da take so sai Yarima, mutumin da nake jin ya gauraye jinin jikina gaba ɗaya.

Hawayena kuwa sun tsiyayo ne ta dalilin wani abu da na ji yana yi mini yawo a tsakiyar kaina. Cikin sakan ɗaya na ga ya ruɗe,ruɗewar da take tayar mini da hankali. Gudun kada ya yi saurin fassara hawayena yasa na koma a hankali na ƙwanta a ƙirjinsa, zuciyata na son gaya masa cewa son da na ke masa yanzu ba zai taɓa misaltuwa ba, amma kunyarsa da nauyinsa sun hana ni sai dai na kurɗa kaina a wuyansa, na ce.

"I love You." Cikin sigar raɗa.

Ina jin shi ya ƙara matse ni a jikinsa,sam ban yi zaton ya ji ni ba, sai na ji ya ce "I love You too." Kunya ta sa na mayar da idanuwana na lumshe. Bai fi mintuna biyu ba na yi ɣar dabara na ƙwace jikina, saboda na san halin Yarima, sai mu ƙwana a haka. Na yi ɗan hanzari.

"Jira ina zuwa, na yi mantuwa." Na sauko daga gadona. Har na yi taku uku ya kira sunana, juyowar da zan yi sai na ji ya ce "I Fancy you."

Na yi murmushi na yi gaba. Faranti ne na shigo da shi ɗauke da abinci, har na ajiye farantin ban ga Yarima ya motsa ba, na yi sanɗa na iso inda yake, ya yi kwanciyar nan tasa, tausayin shi ya kama ni. Ganin kafin in je in dawo har ya yi bacci, na sunkuyo na sumbaci goshinsa, ya buɗe idanuwansa a hankali ya yi murmushi.

"Na gaji."

"I know,sannu ga abinci nan na kawo maka."

Na riƙe hannunsa duka biyun.

"Ta so ka ci." Ya miƙe tsaye a inda na yi gaggawar taimaka masa ya cire alkyabbar jikinsa.

**** **** ****

Lallai kam ni na zama yʻar gata gaba da baya, balle da cikin nan na jikina ya tsufa. Sarki, Mama, Hajiya, Daddyna, Mamee duk ba sa son abin da zai taɓa ni, wanda kullum sai Sarki ya aiko waziri ko jakadiyar sa tazo ta ga lafiya ta. Mamee kuwa, sai dai waya. Dad kuwa ya zo gidana ya kai sau uku, ba wai don ya ganni ba,idan ya ga Yarima sai ya koma. Shi kansa Yarima ya kasa gane kan Daddyna, saboda ko an ce ya shiga ba ya shiga, sai dai ya ce gaishe mu ya zo yi.

Shalelena kuwa, kullum ana manne da ni,ko fada ma sai na yi da gaske yake sauka, Kaɗan-kadan kuwa ya hayo sama balle in ina ɓangaren gidansa,in kuwa na gidana ne, idanuwana na ga barandar gaba wacce ta koma hanyar zuwa ɗakinsa.

Amma wani abu ƙwaya ɗaya da yake damun zuciyata, shi ne yanda gaba ɗaya suka raja'a da cewa namiji zan haifa, ba sa maganar mace ƙwata-kwata , wannan abu na tayar mini da hankali, ballantana idan na ga Yarima ya ɗaga cikin nawa yana sumbatarsa,yana faɗin ɗan shi ya kusa isowa duniya. A take sai na ji hankalina ya tashi, wannan ne ma yasa wasu lokuta na kan yi shiru tamkar na fita daga hankalina na yʻan mintuna.

Buɗe ƙofa da na ji yanzu ma ita ta dawo mini da hankalina, na gyara kishingiɗar da na yi a saman kujerar falon samana, na juya na kalli Yarima wanda ya fito daga ƙofar ƙuryar ɗakina,su Mansura suka yi saurin russunawa suka yi gaisuwa, sannan suka miƙe domin sauka ƙasa.

Ya iso ya tsugunna gwiwarsa ta hannu a saman cinyoyina, "Honey,na bar ki ko?" Ya ɗan yi tsaki.

"Wallahi Mai Martaba ya ƙi yarda, da yanzu muna can, tare da ke kullum."

Ya sunkuyo sosai, "My boy,how are you today?" Yasa hannu ya buɗe cikin kamar yanda ya saba, ya sumbace shi ya mayar da kansa ya ƙwantar a jikina.

Na sunkuyo na sumbace shi, gashin kaina duk ya rufe mu gaba ɗaya. Na ɗaga kaina sannan na ɗago shi.

"Yarima in tambaye ka mana?"

"Ƙwarai kuwa."

"Me yasa ba ka son a haifar maka mace?"

"Me ki ka gani?"

"Ban taɓa jin ka ambaci mace ba,ko ba ƙwa son a haifar muku mata?" Na yi shiru kaɗan.

"Yanzu in na haifi mace ba zaka zauna da ni ba?"

Sai kawai idanuwana suka ciko da hawaye. Ya miƙe tsaye ya zo ya zauna kusa da ni, wanda hakan yasa na saukar da ƙafafuwan ƙasa. Ya kamo hannuna ɗaya ya riƙe da hannayen shi duk biyun ya fara wasa da yʻan yatsun hannuna,a daidai lokacin da ya fara magana.

"Yasmin kin san dai mutum ba ya haihuwar wata halitta wacce ba mutum ba ko? Sai dai ya haifo nakasasshe ko marar lafiyar jiki,ko wanda halittarsa ba ta cika ba,ko kuwa ma ya mutu a ciki ko?" Na ɗaga kaina.

"To wallahi Yasmin a ce ki haifo wata halitta ta daban,ko ɗaya daga cikin abin da na lissafa, wallahi ni na san ma na so shi na gama,ko da kuwa jama'a za su ƙi ni a kansa, saboda kawai ya fito ta jikinki, ta balle mace mutum. Yasmin ya zan yi naƙi mace, alhalin kin san mu mata rahama ne a gare mu.

Ki tuna ke mace ke kika canja mini rayuwata, ta zame mini abin so da ƙauna, abin sha'awa ga kowa. Ke mace ke kika ƙwantar mini da hankalina lokacin da ya tashi, ke mace ke ce kika rungume ni a jikinki a daidai lokacin da na wuce mahaifiyata ta rungume ni a jikinta.

Ki tuna ke mace, ke ce wacce za ta haifa mini yʻayʻana,ki tuna ke ce tsanin rayuwata gaba ɗaya,in kin ga dama ki ruguza min rayuwata, wanda duk duniya babu mai baiwa ɗa namiji daɗin rayuwa sai Allah da matarsa tagari,in kin so kuma ki gyara mini ita.

Yasmin ki ƙwantar da hankalinki a kaina,ki dinga haifa mini yarana,ko da kuwa duk mata ne, ina so. Wallahi ina so,ni na san dalilin ki,wai sarauta? Ba dole ba ne a ce dama ɗana ya yi sarauta,ko da kuwa duk maza na haifa har guda ɗari,in Allah ya so sai ya ba yʻayʻan ƙannena,ƙila ma wanda ba'a ɗakinmu ɗaya ba da mahaifinsa.

Dakata ma ki ji, wallahi ni yanzun tun da na same ki a matsayin matata, na ji komai na duniya ma ba na son shi sai ke, ke kaɗai nake so. Baki san ma ni cewa nake dama a baiwa Ahmad sarautar nan saboda in zama free man in dinga zama da iyalina a kodayaushe muna hira,muna jin ɗumin junanmu."

Ya ɗago ya kalleni, ya juyo sosai. "No! No!! No!!!." Yasa yatsunsa manya biyu yana goge mini hawayen da suka gangaro.

"Shi yasa na liƙewa Mai Martaba a kan ya bar ni na tafi da ke London, muyi rainon cikinmu a can, ya ƙiya mini,ba don komai ba sai don in zamo kullum ina kusa da ke, da na samu haka da wannan tunanin bai ma zauna a zuciyarki ba."

Ya ɗago fuskata muka haɗa ido, sai na ga ya lumshe ido ya buɗe a hankali, ya kai bakinsa ga nawa.

Mintuna biyu ya ɗauka a haka, na yi dabara na cire bakina daga nasa, sanadiyyar wasu alamomi da jikinsa ya nuna mini. Sai da ya ɗauki tsawon wasu ɣan mintuna yana fitar da numfashi a hankali, sannan ya koma ya zauna. Ganin shirun da ya yi yawa.

"Yarima ka manta da ka baro jama'a?"

Ya ɗago ya kalleni sosai, ya lumshe idanuwansa tare da ɗan mayar da numfashi.

"Yanzu zan tafi, ke ce Yasmin,ke ce."

Ya miƙe tare da ɗan shafar saman kaina, sannan ya tafi. Ni kaina na san ina samun kulawa ɗari bisa ɗari a wajen Yarima, da jama'arsa gaba ɗaya. Ban da iyayenmu da suke zirga-zirga a kan ganina. Ni kam yanzu na riga na san Allah ya gama haɗa mini komai, sai dai in yi godiya gare shi.

########

[2/20, 18:49] Ummi Tandama😇: *ƘASAITA BOOK 3*

NA

MARYAM KABIR MASHI

Page 5

Tun kafin a kira sallar Asuba idanuwana suka bushe, sakamakon jin cikina ya naɗe ya tattare waje ɗaya, ya hana mini sakewa. Ina zaune lafiya ƙalau, Yarima ya tashi ganina a zaune yasa na ga ya tashi zaune a firgicen shi yana tambayata ko lafiya? Kafin in bashi amsa ma har ya ɗauki wayar hannunsa ya fara daddana ta. Na yi sauri na ƙwace ta.

"Haba Yarima."

"Me ke damun ki?"

"Ba komai."

"Yana gan ki a zaune, kuma sannan ki ce mini ba komai."

"Tun ɗa na ce ba komai ka yarda,cikina ne kawai na ji kamar an ƙulle mini shi waje ɗaya."

"Na yarda, amma kin san dai daga ni har ke ba wanda ya san wata alama ta haihuwa, saboda haka ki yi mini haƙuri in kirayo Hajiya Kilishi."

"Na yarda, amma ka jira na yi sallah tukunna,ka ga yanzu biyar da mintuna ashirin."

Da ƙyar ya amince, sannan muka tashi muka yi alwala tare, wanda ya yi mini sallama ya tafi masallaci.

Shida da ƙwata na asuba Hajiya Kilishi ta iso gidanmu. Yanda Yarima ke bin ta a baya na yi imani shi ya je ya ɗauko ta har gida. Ya iso ya zauna ɗan nesa daga gefen gado,ni kuwa kallona da shi yʼar harara da take nuna alamun ya yi laifi, bai wani kulani ba na ga ya mayar da hankalinsa ga Hajiya da ke ɗan yi mini yʼan tambayoyi.

Dole tasa ni in tashi tsaye, amma tsayuwa ta gagare ni, ni kuwa ba wani ciwon da nake ji,iyakacina dai ƙuguna ya riƙe gam, cikin jikina ya naɗe waje ɗaya. Ganin haka yasa na ji ta ce wa Yarima ya bugawa Doctor Franca waya, wacce ita ce likitan gidan Sarki, sai kuwa Doctor Harisu, mai duba maza,ko wani ciwo amma haihuwa sai Doctor Franca.

Cikin mintunan da ba su wuce ashirin ba sai ga Doctor Franca ta iso. Ina jin Hajiya na tayi mata bayani kamar yanda na yi mata. Cikin yʼar hikima irin ta su ta likitoci ta aiki Yarima akan ya ɗebo mata ruwa a ɗan wani abu, yanda na ga sun kalli juna ita da Hajiya shi ya tabbatar mini suna son ya ɗan ba su waje ne.

Ai cikina kawai ta dafa ta ce haihuwa ce, sai dai kuma miƙewa tsaye ma ba zan iya ba, ballantana in iya tafiya. Ana cikin haka Yarima ya shigo da wata tasa a hannunsa, ya ciko da ruwa, har bakinta. A nan ne take gaya masa haihuwa ce, amma sai an samo kujerar tura ta zuwa asibiti. A zuciyata na ce yanzu a haka za a kai ni asibiti? Ban ƙarasa tunanina ba sai dai kawai na ga Yarima na shirin ɗauka ta.

Kunya kam ta kama ni, amma ganin Hajiya Kilishi ba ta yi masa magana ba, yasa na lumshe idanuwana kawai. Jin an ɗan tsaya da tafiya yasa na buɗe idanuwana. Labulaye kawai na ga an janye, sai da na waiga ma sannan na gane falon sama

muke,babu wata alamar ƙofa a wajen da suka buɗe labulan. Hajiya Kilishi kawai na taɓa wani ɗan makunnin kunna fitila, sai kawai na ga ƙofa ta buɗe.

Mamaki biyu ya dirar mini a daidai lokacin da muka shiga ɗakin, ban gama mamakin ƙofar ba sai kuma gani na dasa na ɗakin da muka shiga. Ɗaki ne wanda ba su da maraba da na asibiti. Gado biyu ne a ɗakin irin gadajen asibiti, sai daga can gefe ɗaya an saki wani koran labule. Abin ka ga ƙaton ɗaki, ban ƙarasa gani ba naji an ɗora ni saman gado, wata irin kunya ce ta saukar mini a take sanadiyyar sumbatar goshina da Yarima ya yi a gabansu Hajiya.

Madadin in ga ya fita, sai na ga ya zauna gefen kaina,ya sa hannu yana gyara mini gashin kaina, da ya baje fuskata,ko in ce ya baje ko'ina. Madadin in ji sun ce ya fita, sai dai na ga an sako wani ɗan koren labule, wanda ya sauka saman cikina, ma'ana ya raba tsakaninmu da su. Ni kuwa ta kwance sun raba ni biyu suke nufi kenan, kaina da gangar jikina ta sama ta wajen Yarima, daga cikina zuwa ƙafafuna suke wajensu.

Sam ni ban wani tsorata ba, saboda dama ita ke zuwa yi mini awo duk bayan sati biyu, sannan kusan duk ƙwana uku sai ta zo ganina, ballantana ma da cikina ya tsufa sosai. Shi kuwa ganin an yi haka, sai na ga hankalinsa ya tashi matuƙa, har da wani irin gumi da ke tsiyaya daga saman kansa. Ganin haka yasa na sa hannuna ɗaya na shafo kumatunsa, ya juyo sosai ya kalleni cikin sanyin murya, na ji ya yi mini magana.

"Da ciwo ko?"

Gaskiya ni bana jin wani ciwo ko ɗaya, saboda haka na girgiza masa kai alamar a'a. Hannunsa ɗaya da ke maƙale da nawa ya ɗago ya sumbata,ni kaɗai nake jin abin da ake yi mini,amma ba ni da damar nunawa, ganin yanda hankalin Yarima ya tashi.

Ba afi minti ashirin da kawo ni ɗakin ba na haifi yarona namiji, amma ni kaina na san cikin mintunan na fita daga kamannina, shi kuwa Yarima ya sha cakuma tamkar zan karya shi.

Ni kaina ban san duk jama'a sun san ina ɗakin haihuwa ba, sai da na fito. A nan ne na ga falon sama cike da jama'a. Ina fitowa kuwa bakuna suka dinga haɗuwa wajen yi mini sannu, ban da jakadiya wacce ta rangaɗa guɗa tamkar ta yi hauka don murna. Yarima ne ɗauke da yaron naɗe cikin jakar tawul ɗin jarirai, amma sai da jakadiya ta tsugunna ta karɓe shi daga hannunsa.

Ni kuwa na sha gayuna tamkar ba ni ce na haihu ba. Tun daga ranar kuwa shagali ya tashi, amma kuma Yarima yana liƙe da ni,in ka ga ya fita daga ɗakina,dangin mahaifiyarshi ne ko nawa, shi ma yana yi yana zagayowa.

Ana saura ƙwana biyu suna aka kai wa Mai Martaba jariri har gida, domin yi masa huɗuba, wanda taro suke yi na musamman idan za'a huɗubar nan, duk da dama ba ganin farko ba ne ba ga Mai Martaba, domin jakadiya ta kaiwa Sarki jaririn da Mama tun ranar da aka haife shi. Haka kuma Daddyna shi ma an kai masa shi gida.

Wani abin mamaki kuma shi ne yaron kamar su ɗaya da Mai Martaba Sarki, ba ni da wani bakin magana sai dai kawai na yi wa Allah godiya, na yarda aka nuna mini ƙauna.

Shi kuwa Yarima tamkar yau aka kai ni gidansa, saboda irin yadda yake liƙe mini. Maganar mai taya ni zama kuwa, Yarima sam ya hana mata sakewa, saboda sai ta yi barci, sai kawai na ji shi rungume a jikina,ko da kuwa zan kulle ƙofar barandar bayan ɗakina, sai yasa mukullin ya buɗe.

Tun saura ƙwana biyu suna gida ya ɗauki cika, duk da Mai Martaba yasa a buɗewa jama'a gidan baƙi. Daren suna kuwa, abin har tsoro ya ba ni, irin yawan jama'ar da ke ƙwararowa gidanmu, ban da kaya da aka dinga shigowa da su,wai duk nawa ne ni da jaririna.

Ba zan iya gane ko ƙarfe nawa na dare ba, amma tabbas na san dare ya soma yi sosai. Cikin ɗan sauri na tashi zaune, ina lalubar gabana inda jaririna ke ƙwance, amma ban ji kowa ba,gudun kada in kunna fitila mutanen da ke ƙwance ɗakina duk su farka, yasa na yi amfani da fitilar wayata, amma ban ga jaririna ba. Na haska gaban Aunty Salwa da take ƙwance kusa da ni, sai ƙaton goyon ɗanta a gabanta.

A hankali na miƙe na dinga haska gabanta ina haska gaban baƙin da ke ƙwance a manyan katifu a tsakar ɗakina, duk da yaƴan ƙannai da matan yayye da yaƴan uwan Mamee, amma duk ba jariri a tare da su.

Na bi a hankali na buɗe ƙofar shiga sama, saboda duba su jakadiya da mata biyun da suke taya ni ƙwana da yaƴan hidimomi ni da jariri. Duk na haska gabansu babu alamar ƙaramin yaro a tare da su.

Sam ni ban ruɗe ba saboda na san da wuya a sace yaron nan, sai dai abin da na yi tunani ko dai suna wata al'adar ne wacce sukeyi da tsakiyar dare. Har na koma na ƙwanta sai na ji na kasa bacci ni kaina, ban san ina son jaririna ba sai yanzu. Na miƙe cikin sanɗa a hankali na buɗe durowar da alkyabbobina ke rataye na sanya ɗaya saman rigar barcin jikina.

Ban yi wani motsi da ƙarfi ba har na samu na buɗe barandar ta wacce zata kaini dakin Yarima, domin in sanar masa abin da ke faruwa. Ina buɗe ƙofarshi da makulli ba abin da na ci karo da shi sai ɗan sayon sayon safar jaririna ɗaya. Na sunkuya na ɗauka, sannan na ƙarasa cikin ɗakin.

Fitilar wayata dai na yi amfani da ita ina duddubawa, na yi murmushin da ya ratsa har zuciyata, saboda jin daɗi. Na lallaba na isa inda suke ƙwance. Ƙwance yake a rigingine ya ɗora yaron a ƙirjinsa, fararen kayan sanyi ne ya sakawa yaron,zaman da na yi a gefensu wannan yasa na kunna fitilar gefen gadon da suke ƙwance. Ƙyau Yarima ya ƙara yi mini. Na sunkuya na sumbaci goshinsa, tare da shafa gashin kansa.

Gani na yi ya buɗe idanuwansa a hankali, "Ka firgita ni fa."

Ya yi yar miƙar nan ta masu bacci, sannan ya tallabe yaron, ya miƙe zaune tare da sa ɗaya yana murtsikar idanuwansa alamar tashi daga bacci, har da yar guntuwar hammarsa. Zolaya ta sa nayi alamar tashi in tafi, sai a lokacin ne ma ya yi magana.

"Ina za ki kuma?"

"Ɗakina."

"Da me ya kawo ki?"

"Neman yarona."

"Shi kaɗai ya dame ki,ni fa? Ko yanzu ba'a yi da ni?"

"Na isa."

"Zo nan."

Ya nuna kusa da shi da hannu ɗaya. Na iso na zauna.

"Dama na ɗauko shi ne saboda ina son yin magana da ke,kin ga da wuya gobe mu samu ganin junanmu da zamu iya tsayawa mu yi magana, saboda jama'a.

Dama game da sunan yaron nan ne. Mai martaba ya mayar masa da sunansa, shi ne na ce bari na tambaye ki in ya yi miki,kin san shawara tana da daɗi."

"Yarima ba ka gajiya,in ba ya ga zolaya irin wacce ka saba yi mini,ya ma zaayi in buɗe baki in ce bana son sunan da Sarki ya sa. Kai dai ka faɗi maganar da ke damun ka, ba dai wannan ba."

"Ita ce mana, sai kuwa maganar zuwa gida wanka, gidan mu fa ake kaiwa, ma'ana wajen Mama za'a kai ki, gidan Sarki, amma za'a tambaye ki ra'ayin ki."

Ya kama hannuna ɗaya, "Don Allah ki ce nan za ki zauna,a kawo miki masu kulawa da ke kawai,kin san Allah ko jakadiya kawai sai ta kula da ke, ballantana daga gobe kin gama wankan ganyen, magunguna zaki cigaba da sha."

Na yi shiru, tunanin ya za'ayi in ce bana zuwa. Na girgiza kaina.

"Ba zan iya ba, kunya nake ji."

"Kunyar me, ba gidan mijinki ba ne ba."

"Saboda me kai kuma ka ke son in Zauna nan gidan."

"Saboda ni."

"Ba ka da lafiya ne?"

"A'a,in dinga ganin ku."

"Ai can ma zaka dinga ganin mu ko?"

"Yasmin, Please understand me."

Na miƙe tsaye, "bari in tafi kada wani cikinsu ya farka bai gan ni ba, kaga kunya zan ji."

Bai ce mini komai ba, ya koma ya ƙwanta. Ni kuwa na juya na nufi ɗakina, amma sai na ji duk jikina ya yi mini nauyi.

Da na ƙwanta kuwa har gari ya waye ban yi bacci ba, saboda tunanin maganar Yarima ina son in ga jakadiya in gaya mata, saboda ko tana da dabarar yi, amma jama'a sun yi yawa.

"Subhanallahi!" Na faɗa a zuciyata, saboda ganin yanda jama'a suka yi yawa, har sun fi duk taron da aka yi. Cikin gidan kuwa jama'a mata da maza,cin abinci akeyi ban da kayan sha,kai abin ya yi mini yawa, har na zamo ba na iya gane komai.

Daɗina ma ɗaya ba yawo ake yi ba, zaune nake a saman kujerar mulkina a falon ƙasa, sai dai kowa ya zo ya kawo tashi gaisuwar,in kuwa na miƙe tsaye, to kaya zan je sakewa. Jariri Jafar Bn Jafar,yana hannun yayar Mamee Ruƙayya a riƙe, sai dai a leƙa a gansa, wanda kuwa yake da buƙatar ganinsa sosai sai dai ya kalli ƙaton hotonsa da ke manne a falona, wanda Mai Martaba ne ya aiko da shi.

Ƙarfe huɗu na yamma kuwa duk jama'ar da ke gidan mu ta dawo waje, ana gama sallah kowa ya nemi wajen zamansa, tamkar dai yanda suke yin kayansu, amma yanzu ya sha bamban da na baya, tunda na baya za ka ga jama'a bayan mu, yanzu kuwa daga ni sai Yarima, sai kuwa dogarawa guda bakwai da ke zagaye da mu.

#####

[2/21, 08:11] Ummi Tandama😇: *ƘASAITA BOOK 3*

NA

MARYAM KABIR MASHI

Yaro Jafar Bin Jafar na hannun jakadiyar Sarki, tsaye wajensu Mama da Mamee da Hajiya Kilishi, ban da ragowar mutanen da ke bayan su. Dad ɗina kuwa ga kujerarsa ga ta Sarki.

Wasan ƙwallon dawaki aka fara yi (Polo), sai kuwa ɗan hawan Daba, sai wani wasa da shanu ke yi (Hawan Ƙaho), ban da wasanni da raye-raye da yare kala-kala suka yi. Saboda Yarima dai shi ne baya magana, amma ta hannu da ta ƙafa yake yi mini magana, shi ne yatsun hannuna ɗaya na riƙe da nashi yana ta wasa da su, ban da idan na gaji na ƙwace ya koma tsokanar ƙafa.

Duk bayan an gama wannan hidimomin ne wanda za mu iya cewa ƙarfe biyar da rabi ta yi, sai na ga wasu irin ƙartin mutane guda biyar sun shigo filin, kowanne ɗaure da bantai a jikinsa, ma'ana ba riga sai wata fata mai ruwan jinin kare ɗaure a ƙugunsu, ga shi iyakacinta cinyarsu.Waziri ne ya miƙe ya fara magana.

"Yau ne ranar da Allah ya kawo muka ga jikan Mai Martaba Sarki, rana ce ta farin cikin kowa. Duk wani wanda yake gidan nan ya san sunan yaron shi ne Jafar Bin Jafar, wanda ya gaji sunan Sarki kenan. Yanzu za mu ƙara tabbatar da cewa yaro namu ne, jinin mai girma Yarima ne, duk kuwa wanda ya tashi a gidan nan ya san ƙa'idarmu ce hakan, saboda haka jakadiya Bismillah."

Ni dai na sa ido in ga ikon Allah, na san kuwa ba ni kaɗai ba, har danginmu gaba ɗaya, shi ne yan uwan Mamee da Daddyna.

Jakadiyar Sarki ta sauko daga sama riƙe da jariri a hannunta sanye da kayansa masu ƙyan gaske. Tana shigowa tsakiyar filin nan sai na ga ta miƙawa ɗaya daga cikin ƙartin nan ɗana. Na ɗan yi alamar zan miƙe, Yarima ya riƙe min hannu. Ban ko kalleshi ba, amma na san dai na koma na zauna.

Ina kallo aka tuɓe (cirewa) yarona kayansa gaba ɗaya, ya zamo tamkar yanda aka haife shi. Ganin ƙaton nan ya cilla jaririna sama yasa na yi saurin cakume cinyar Yarima da hannuna ɗaya. Sai a lokacin na ji Yarima ya yi magana, sai da ya jefa shi sama sau uku yana cafewa, sannan na ga ya miƙawa tsohon cikinsu.

Me zan gani? Gani na yi ya saka mini yarona a cikin ruwan nan da ke cike da uban bahon ƙasar nan,ai ban san lokacin da na miƙe tsaye ba na ce "Yarima kalli ka gani, za'a kashe shi." Da sauri na ga Yarima ya fizgo hannuna ya zaunar da ni.

"Yasmin ki ƙwantar da hankalinki, kada ki ba ni kunya. Ni nayi imanin Jafar ɗana ne,ni ne mutumin da ya fara sanin Mamansa,ni na san...."

Ai kuwa wannan tsohon mutumin yasa yarona cikin ruwan nan ya barshi ciki bai ɗauko shi ba. Yarima ya matsa hannuna sosai, "Kalle ni." Na juyo na kalleshi.

"Me ki ka gani?"

"Ba komai." Na juya na kalli inda aka jefa mini yarona.

"Ka gani ko,ka gani ko." Jin ya yi shiru ya ƙyale ni yasa na yi saurin kallonsa.

Fuskarshi ba wata walwala da ya juyo ya kalleni. Ni kuwa har firgita na yi don tsoro, wannan yasa na yi shiru na zauna sosai, sai kuma hawaye da na ci gaba da zubarwa. Ba wani mai ƙwaƙƙwaran motsi a cikin mutanen da ke wajen nan, wajen ya yi shiru kowa yana kallon ikon Allah, tamkar a ce wani shugaban ƙasa ya iso wajen taron,an tashi za'a yi taken ƙasar su.

Abin ka ga uwa, sai na ji na kasa haƙuri, sai da na ƙara kamo hannun Yarima,ko kallona ma bai yi ba, na juya na kalli Dad ɗina,amma ban ga alamar hankalinsa ya tashi ba, kowa na kalla sai in ga hankalinsu ƙwance yake, sai dai alamun su da ya nuna suna jiran ganin abin al'ajabi.

Sai da aka ɗauki tsayin mintuna wajen sha biyar, sannan na ga yasa hannu ya ɗauko shi. Yanda aka yi masa da farko, haka ya yi masa yanzu, shi ne cilla shi sama sau uku. Inda na ga kamar hankalin Yarima ya tashi, shi ne a inda aka cilla shi na

farko, sai na ga Yariman ya ɗan yi alamar miƙewa tsaye, na biyu sai na ji yasa kuka irin nasu na jarirai, sai na ga Mai Martaba ya miƙe tsaye.

Gaba ɗaya mutane suka miƙe tsaye aka dinga ihu da tafi,sai a lokacin na ga Yarima yana dariya, ya juyo ya kalleni, kallon da ni da shi kawai muka san fassarar shi. Hankici ya miƙo mini, ma'anar shi na goge hawayen fuskata, tare da cewa.

"Na gode." Cikin sanyin murya.

"Wata al'ada sai mu masu ita."

A nan na ga jakadiyar mu ta gangara tsakiyar filin nan, jakadiyar Sarki na karɓar yaron sai na ga ta baiwa tamu jakadiyar. Murna kuwa da jakadiyar mu ke yi kamar zata kifa don sauri.

Daga nan dai jakadiya ta ɓace mana, sai kuwa Sarki da ya tashi ya yi wa jama'arsa godiya tare da ni kaina da iyayena.

Ana haka aka miƙo mini jariri Jafar,wai zan kai wa Sarki shi. Kamar na yi ihu don kunya. Ganin na kasa tafiya yasa Yarima ya karɓa, ina kallo ya miƙawa Mai Martaba, shi kuwa ya ɗan tsaya yana nunawa jama'a shi, sannan na ga ya miƙawa wazirinsa.

Jafar ya yi lamo cikin baƙaƙen kayan sanyi, waɗanda aka ɗorawa ƙaramar alkyabba a sama. Waziri ya miƙawa Hajiya Kilishi wacce suke rukunin mata Iyaye. Ina kallo ta baiwa Mamee. Mamee da ƙyar ta karɓa,ni dai na san kunya hana ta karɓa tun farko.

Bai fi na mintuna biyu ba ta miƙawa Mama. Mama ce ta kaiwa Daddyna, inda na ga Daddyna ya karɓa yana dariyar farin ciki, irin wannan dai aka ci gaba da yi har lokacin sallar Magriba ya ƙarato, aka rufe taro da addu'a aka tashi.

**** **** **** **

Gama arba'in ɗina da ƙwana uku, ya yi daidai da hidimar bukukuwan barorin gidanmu,yʻan mata da samari, wanda su Mansura tun da biki ya matso take kukan rabuwa da ni, duk da an ce wa mazajen su mai so zai iya barin matarsa ta yi aiki, ana biyanta kuɗin aikinta.

Bayan ba kuɗin mota za su dinga biya ba, gidaje ne aka gina musu a cikin dajin gidanmu, sai dai na san muna da ɗan nisa da su.

Ana gobe kai amarya ne na taka gidan yari tare da ɗana Ammar, wanda yake ɗauke ga kafaɗar Mansura amaryar Isma'il.

Gaba ɗaya na sa aka jera su layi, na dinga tambayarsu. Yawanci laifi ɗaya gare su, shi ne rashin kunya, wasu kuma sun tarewa Yarima hanyar fita,babu dai wani taƙamaiman mai laifi, sai mutum tara,su ne aka haɗa baki da su za'a sawa Yarima guba a abinci, Allah ya toni asirinsu.

Macen da na samu lokacin da Yarima ya kawo ni gidan yarin, ita kuma laifinta shi ne ta aiko da takarda tana son Yarima, shekarunta ba su wuce ashirin da huɗu ba, sai dai yʻar wahala ce ta mayar da ita baya kaɗan.

Gaba ɗaya mazan na sallame su,ban da taran nan, kowanne daga cikinsu na bashi jarin dubu ashirin da kekunan hawa. Su kuwa matan keken ɗinki da dubu goma-goma. Mubaraka ce kawai na ce a kai mini ita gidana da sauran tambayoyin da zan yi mata. Mazan nan tara kuma na ce a tsare mini su, sai na yi bincike a kansu.

Wata ɗaya na baiwa Mabaraka akan ta fito da miji a yi mata aure,in kuwa ba haka ba duk abin da ya biyo bayan haka, ita ta janyowa kanta. Na kawo dubu biyar na bata ta sayi sabulu kafin ta fito da miji.

An yi bukukuwa lafiya, taro kuma ya tashi lafiya, amma inda Allah ya ba ni sa'a har yau ina tare da yarana na gidana, duk mazansu sun bar su, sai dai wasu biyu da aka

kawo mini saboda ƙwana. Ammar kuwa ya zama abin ƙauna ga kowa. Yarima kuwa,ni da shi tamkar amarya da sabon angonta.

**** **** ****

Ƙwanciyar hankali tana neman gagarar mu ni da mijina, da duk wani masoyinmu, sakamakon juya bayan da Sarki ya yi mana,a cikin wata biyu kenan. Dabara, hanyoyin daidaitawa duk mun bi su amma abin ya faskara. Wannan tashin hankali ya hana mini Yarima iya zama gida, kullum yana gidansu neman ko a shirya, amma al'amari sai ma gaba yake yi.

Babu wanda idanuwana ke son gani sai Yarima, saboda tun asuba da ya fita bai dawo ba, sai dai ya yo waya cewa Sarki na son ganinshi, gashi har ƙarfe goma na dare ta kusa. Tun ina hira da mutane har na kai ga komawa falon sama ina zaman jigum ɗin isowar Yarima, amma babu tunanin da nake sai na maganganun da jakadiya ta gaya mini.

Anya kuwa jakadiya ba nema take ta zura ni hanyar wahala ba? Na tunano yanda ta ce mini,wai in dage da abi..... Shigowar Sa'a ita ta katse mini tunanina,tare da jin kukan Ammar. Tana isowa ta durƙusa ta miƙo min shi. Ban tsaya jiran wani ba'asi ba na raɓa shi a cinyata, domin ba shi abincinsa da ke jikina. Ita kuwa ta yi mini sai da safe ta juya ta koma maƙwancinta.

Wasa irin na ɗa da mahaifi, shi Ammar yake son mu yi, shi ne riƙe bakina da yi mini waƙar yarensu ta yara, amma yau na kasa kula da shi. Yaron da Babansa ya sangarta shi da wasanni kala-kala, ballantana da ya fara girma.

Hankalina kam ya tashi matuƙa, ganin agogon falon ya nuna sha ɗaya har da minti ashirin, amma ban ga Yarima ya dawo ba, wannan ne ya ba ni damar tashi na nufi sashensa, tallabe da Ammar a saman kafaɗata, yaran da ya yi bacci wajen awa ɗaya kenan.

Gabana na ji ya yi wata irin mummunar faɗuwa,jin ƙofar barandar bayan ɗakin Yarima a kulle, na saka nawa mukullin, amma da ɗan makullinsa a jiki.

Me Yarima yake nufi? Ba ya son ganina ko kuwa? Har na ji raina ya yi mugun ɓaci hakan yasa na dawo ɗakina na shinfiɗar da Ammar na zauna na rafka tagumi.

Zuciyata babu abin da bata saƙa mini ba,amma daga ƙarshe duk na ajiye zugar shaiɗan ɗin da ta yi mini,na miƙe na ɗauki alkyabbata na saka, tare da tallabar Ammar. Shiru gidan namu sakamakon kowa ya yi bacci, sai masu gadi da suke yawo.

Ƙofar gidan Yarima a kulle take, amma saboda ina da makullin ƙofar a cikin makullaina yasa na sa na buɗe ta,yau ko y-ar fitilar nan da ake bari ta falo ma babu ita, security light. Cikin ɗan lalubar hanya na iso falon shi na sama, shi ma fitilar wajen a kashe take, na murɗa ƙofar ɗakinsa na shiga.

Nan ma fitilar ɗakin a kashe suke, na sa hannu na dinga laluba inda makunnin wutar yake da ƙyar na samu na gano shi. Haske ya gauraye ɗakin, wanda ya yi daidai da haɗa ido da Yarima, mutumin da na gani a ƙwanciyar rigingine, amma gaba ɗaya ƙafafunsa a ƙasa suke,gangar jikinsa ce kawai ke saman gado. Ya dinga kallona,ni kuwa na yi tsaye ina neman iso. Bai yi mini magana ba, amma ya yi mini magana da kansa, alamar in zo in zauna kusa da shi.

Wata zuciyar ta ce in juya inyi tafiyata, amma sai na yi tunanin hakan ba mafita ba ce. Na isa na zauna kusa da shi, kamar yadda ya umarce ni. Na juya na kalleshi tare da dafa hannunsa ɗaya. Wannan na lura ba ƙaramin daɗi ya yi masa ba, sakamakon tashin da ya yi zaune, tare da ɗauke Ammar daga cinyata,yaro ɗan wata baƙwai da haihuwa.

Ya miƙe tsaye ya kai shi,saman gadonsa ya shinfiɗe shi, sannan ya dawo ya tsugunna gabana, tare da kama hannayena duk biyun. Ganin ya kasa yi mini magana yasa na kama shi ya miƙe tsaye.

Cikin nutsuwa na mayar da shi na ƙwantar a saman gado. Abubuwan da na san za su karkato da hankalinsa zuwa gare ni shi na dinga yi masa cikin salo-salo, hankali ƙwance. Yarima cikin sauri jikinsa ya ɗauki rawa, wacce take ba ni tsoro a duk

lokacin da ta zo masa, amma yau zuciyata na ji ta yi mini daƈi, saboda na samu hanyar da zan tambaye shi me ke faruwa.

Tabbas Yarima ya nuna mini farin cikinsa a fili har na tsayin wajen minti arba'in. Fitilar gefen gado ya kunna, sakamakon duhun da ya gauraye ƈakin a ƈan tsayin mintunan da suka wuce. Ina kallo ya miƙe yasa alkyabbarsa,nima ya ƈago ni ya miƙo mini tawa.

######

[2/22, 15:44] Ummi Tandama😇: *ƘASAITA BOOK 3*

NA

MARYAM ƘABIR MASHI

Yanda ki ka san kurame muka koma saboda kamo ni ya yi ya durƙusar da ni gabansa, sannan shi ma ya durƙusa, ma'ana ɗai mun haƈa gwiwoyin ƙafafun mu waje ƈaya,muna fuskantar juna. Ya kama hannuna duk biyun, sannan na gaya sunkuyar da kansa. Ganin ya ƈan ƈauki lokaci bai yi magana ba,yasa na zame hannuna ƈaya na matsa sosai, na tallabi kumatunsa ƈaya, sannan na ce, "Yarima." Cikin sanyi murya.

Wannan ya ba shi damar yin magana, "Yasmin." Ya yi shiru.

"Yasmin,zaki iya zama da ni ko bani da sarauta? Ko ba ni da komai,ko kowa zaya ƙi ni,ko bani da masu yi miki hidima? Ko ba ni....."

Hannu na sa na rufe bakinsa, "Yarima ka daina shakku a kaina,ni kai nake so,ba wani abin ka ba, ba kuma wani naka ba, zan zauna da kai Yarima a duk halin da ka shiga, ballantana na sanar har abada ba zaka taɓa taɓewa ba,tun da tun farko Allah ya nuna maka ƙauna a kan harkokin rayuwarka. Shin wai taƙamaimai me ya janyo wannan rashin jituwar tsakaninka da Mai Martaba ne? Anya ba ƙulli? Mai Martaba na sonka,son da kowa yake son ya ga iyayensa na yi masa."

"Yasmin,idan na ce miki ga abin da ya haɗa mu nayi ƙarya. Ni dai an wayi gari ranar wata juma'a mun je Masallacin juma'a na ga Mai Martaba bai damu da ni ba, kamar yadda yake yi mini da. Da aka tashi na je gaishe shi, sai bai amsa mini ba. Ban damu ba, saboda na yi tunanin jama'a ce ta yi masa yawa, saboda haka na yanke shawarar bin shi gida domin yi masa gaisuwa ta musamman.

Ina shiga fadar sai cewa ya yi in fita. Amma a lokacin na yi zaton ɗan wasa ne na tsakanin ɗa da mahaifinsa, amma ina kin ga yanda ta kasance mana yanzu, na koma sai dai in hango mahaifina daga nesa. Jama'a sun sa baki, amma lamarin sai ƙara jagulewa ma yake yi." Ya koma ya zauna sosai, tare da janyo ni jikinsa.

"Yau lamarin ya yi zafi Yasmin,saboda yau Mai Martaba ya ce na fitar masa daga gida, komai ke cikin gidan bai ce na ɗauka ba, face sutturun mu, sai kuwa motar da Waziri ya ba ki."

Ya gyara ya janyo mukulli daga aljihunsa.

"Kin ga waɗannan mukullan, Waziri ne ya ba ni su,wai gida ne gare shi a Sultan Road Kaduna, ya ce na je can na zauna.

Yasmin kunyar ki ta hana ni shigowa inda ki ke, da tunanin kada in gaya miki ki guje ni, kema,ni na san hankalina ya tashi matuƙa, koma in ce yana cikin tashi.Amma rabuwata da ke sai ya fi nakasa mini rayuwata, saboda yanzu al'amarin ya zo da ɗan sauƙi, tunda duk yan fada na sona, kuma har yanzu ba su goyi bayan Sarki

ba,su ma kansu suna mamakin abin da ke faruwa, dukkansu kuma suna iya ƙoƙarinsu, amma al'amarin sai haƙuri."

Ya yi ɗan shiru. "Ni yanzu Mama kawai nake ji, tunda ya ce Allah ya isa idan na shigar masa gida. Yanzu ban san yanda zan yi in dinga ganinta ba, balle in yi sallama da ita a yanzu, saboda plan ɗina in bar ƙasar nan kawai,in koma Greece shi ya fiye mini ƙwanciyar hankali. Ni dai tun da kina tare da ni da sauƙi. Mahaifiyata kawai nake tausayawa."

Yanda gabana ke faɗuwa idan har ka saurara kana ji, saboda tashin hankalin maganar da Yarima ke yi mini. Hawaye kuwa da ke fita a idanuwana, duk sun jiƙe gaban rigata. Jin har ya gama amma ban yi magana ba, shi yasa na ga ya ɗago kaina, sai na ga ya yi murmushi mai haɗe da takaici.

"Yasmin,kada ki tayar da hankalinki, komai ki ka ga ya yi tsanani, to sauƙi na tare da shi."

"Yanzu yaushe ya ce ka tashi?"

"Gobe. Yau fa har wajen manyan shi muka je, amma cewa ya yi muddin Azahar ta yi gobe in har ban tashi ba, duk abin da ya faru da ni ni naja."

"Mama ta sani?"

"Eh, na aika mata da Waziri, sannan na yi mata waya, ta ce in tashi kada ya wulaƙanta ni a gaban jama'a. Yasmin na rasa abin da ke yi mini daɗi a rayuwata. Ni yanzu ya ya ma zan yi?"

Cikin ƙarfin hali na tashi zaune na kalleshi sosai, wanda taimakon Innalillahi ya yi min shi tare da tunano abin da Allah (S.W.T) ke cewa cikin littafinsa mai tsarki:

Fa innama al'usrin usra." Ma'ana:--- _Lallai ne tare da tsananin nan da akwai wani sauƙi, lallai ne tare da tsananin nan da akwai wani sauƙi."_ saboda haka idan ka ƙare (ibada) sai ka kadu kana roƙon Allah, kuma zuwa ga ubangijinka ka yi ƙwaɗayi.

"To yanzu ke wacce shawara ki ka ga ta dace da mu? Mu bar ƙasar ko? Saboda ni abin kunya ne...."

"Sam ba ka tare da abin kunya har abada. A shawarata ka bi maganar Waziri, ka zauna Kaduna,kana jin me ke faruwa, sannan duk ranar da mahaifiyarka ta so ganinka za ta zo har inda ka ke. Yanzu tashi za kayi mu ƙwashe duk kayan mu tun yanzu,muna da motoci,a hannunmu kafin gobe a ƙwace. Kada mu gayawa yaranmu abin da ake ciki,mu ce masu tafiya ce ta kama mu, shekara ɗaya za mu je mu dawo kawai. Yanzu kuma ka tado direbobinmu su kai mana kayanmu Kaduna tun cikin daran nan, ina ga shi ne rufin asirinmu."

"Haka za'ayi, tashi ki kirawo jakadiya ki gaya mata komai, ta taimaka miki haɗa kayanki da na Ammar. Kayan sawa kawai, sai kayan ƙwalliyarki, amma na jiki,sarƙoƙinki, daga su kada ki taɓa masu komai. Kafin ku gama nima na gama haɗa nawa."

Na ce, "To."

Na tashi na tafi, wanda har na kai ƙofa na ji ya kira sunana. Ina juyowa ya ce in jira ya rakani dare ya yi.

Jakadiya na kuka tana haɗa kayanmu. Ban da Ammar da ke goye a bayanta,kaɗan-kaɗan kuwa ta ce, "Amma tare zamu tafi ko Gimbiya?" Sai dai in bata amsa da, "Sai abin da Yarima ya ce."

Ƙarfe huɗu na dare mun gama komai, har direbobin sun tafi da kayanmu. Abin da ya rage a hannunmu aƙwatin duniyarmu da ƴan kayan da za mu sa da safe.

Gari na wayewa tun wajen ƙarfe taƙwas gidanmu ya ruɗe da kukan sallama. Mun yi wannan dabarar ne ta barin gida tun safe domin mu samu a kai mu cikin motar gidan nan, tare da tawa motar da Waziri ya ba ni.

Ƙarfe tara da rabi muna falon Daddyna,yana yi mana nasihohi tare da yi mana alƙawarin za su yi iya ƙoƙarinsu su binciko me ke faruwa. Sannan ya yi mana alƙawarin kai mana ziyara. Ya Kawo addu'o'i ya bamu, ya ce mu dage sosai a kan yin su, Allah zai bayyana ainihin gaskiyar abin da ke faruwa.

Mamee ma haka ta yi mana ita da Aunty Salwa,sannan suka yi mana alƙawarin za su zo cikin sati na sama, domin ganin inda muka koma. Suka yi mana nasiha a kan mu zauna lafiya kada mu kuskura mu baiwa wasu fuska su shiga tsakaninmu, sannan kada mu yarda wannan abun da ya faru ya kawo mana raini a tsakaninmu. Haka dai muka rabu kamar in ce ba zan je ba, amma ganin yanda Yarima ya zama cikin ƙanƙanin lokaci yasa na ji ba zan iya ba.

Sai da muka wuce garin Fambigowa cikin wani ɗan daji, sai muka hango mota jib baƙa da wata ruwan shanshan bale Honda Accord. Wasu mutane suna ɗaga mana hannu. Dalilin ganin mu kuwa direbanmu ne yake faɗa mana shi ne har ya jamu.

Yarima ya ce ya sauke gilasan mu gani, sai da muka iso daidai su, sai na ji Yarima na cewa wai kamar motocin gidan su. Muna dawowa baya Mama na fitowa daga jib ɗin nan baƙa.

Ana cewa tsakanin ɗa da iyaye sai Allah, na amince,yau Mama tamkar zata mayar da Yarima ciki. Tun kuwa da ta karɓi Ammar ba ta miƙo mana shi ba,yana saɓe a kafaɗarta, suka dinga hirarsu ta abin da ke faruwa. Ƙarshe dai Mama ta ce mu dawo motarta mu bayar a mayar wa da Sarki da tashi.

A motar Mama muka isa har Kaduna unguwar Sultan Road,ko awa ɗaya ba mu yi ba da zuwa muka ji ana ta odar mota a get ɗin gidan.

Ɗaya daga cikin direbobin da suka kawo mu ya je ya buɗe ana buɗewa muka ga Jeep Itama baƙa. Joseph wanda direban Daddyna ne, shi muka gani. Ya zo ya

durƙusa ya gaishe da Mama da Yarima, sannan ya miƙawa Yarima makullin da ke hannunsa.

"Dama Alhaji ne ya ce in biyo ku a baya in kawo maka wannan. Tirela kuwa kayan ku ne,a juye a bamu ita mu koma da ita, ya ce kuma idan kuna buƙatar masu aiki ku gaya mani a kawo muku."

Anan ne na ji Mama ta yi magana, "Ka ce an gode, amma masu aiki har na tanadar masu su, har da maigadi ma. Motar ma da na tanadar masu, amma tun da ya riga ni kawowa shi kenan, ta shi za'ayi aiki da ita."

Tasa hannu a jaka ta miƙa masa bandir ɗin kuɗi, sannan ta ce su je su sauke kayan.

Nasihohi da nuna mana cewa abin da ke faruwa jarabawa ce daga Allah, duk shi Mama ta yi mana, sannan ta yi sallama da mu tare da cewa duk lokacin da ta so ganinmu za ta zo, sannan duk abin da ya shige mana duhu ga waya nan a buga mata. Ban taɓa ganin kukan Yarima na gaskiya ba sai yau. Yau har sai da na ji hankalina ya yi matuƙar tashi. Da ƙyar na samu na lallashe shi, shi Ammar har da kuka, na ba dalili,a nan ne na nemi kukan Yarima na rasa.

**** **** **** **

Saboda son junanmu da ƙwanciyar hankali ta ƙaru tsakanina da Yarima, babu inda yake zuwa sai gonar kajinshi da shanu da sauran dabbobi da yake kiwo. Daga can kuma ya isa fadamarsa inda yake noman rani, shi ma sai bayan sallar la'asar yake zuwa, kafin magriba kuwa ya dawo gida kullum. Mu kuwa kamar yara muke ga iyayenmu. Sarki ne kawai har yanzu bai yaye mana abin da ya faru ba. Shekaru huɗu kenan har da watanni biyar.

Yanzu haka bai san mun haifi yarinyarmu mace ba, mai sunan Mama, wacce muke kira da Suhailat. Ammar kuwa tuni an sa shi a makaranta. Wani abin mamaki kuma har hutu yake zuwa Jos wajen su Mamee, har kuma ya isa gidan Sarki ya yi ƙwanansa, amma sai dai Mama ta ce ɗan ɗiyar ƙanwarta ne,wato jikanta ne.

Mu kam Kaduna ta karɓe mu,bamu cikin wata matsala,sai ƙaruwa da muke yi. Shi ne yanzu ana zuwa har gida ana koya mana karatun litattafan addini ni da Yarima. Ga shi kuma yanzu ya iya neman na kansa, wanda a da sai dai ya ga kuɗi bai san ta yadda ake samun su ba.

Yau ma Yarima na ƙwance a doguwar kujera daga shi sai singileti fara da dogon wando,ni kuwa ina ƙwance,wato saman jikinsa,muna ta hirarmu ta yaushe zan je Jos, saboda na samu shekara kenan har da wata biyu ban je ba. Na fahimci Yarima yanzu ba ya son ana yi masa hirar Jos, amma ni a wajena ta zama dole. Bai kai ga bani amsa ba muka ji sallama.

Na ɗan yi gaggawar tashi zaune, sannan na ce, "A shigo." Sa'a mai rainon Suhailat ce ta shigo ɗauke da Suhailat yarinyar da ta shekara ɗaya da wata huɗu kenan. Ta durƙusa har ƙasa sannan ta ce, "An yi baƙuwa tana waje. Na tambaye ta sunan ta domin inzo in gaya maku, amma ta ce ace baƙuwa ce daga Jos."

Nan take Yarima ya ɓata rai, "Ki ce mata ta koma can Jos ɗin, nan gidan duk yɑn Kaduna ne ba yɑn Jos."

"A yi haƙuri Yarima." Ya juyo da saurin gaske, ya kira sunana. "A yi haƙuri kuskure ne,je ki kice ta shigo." Ta tashi ta fita.

Kafin ta shigo na yi saurin miƙa masa doguwar rigarsa ta shan iska. Ya karɓa tare da yi mini ƙorafin kada in ƙara kiransa da Yarima, baya so. Na bishi da na daina.

Wata fuska na gani, wacce da gani na san fuskar, sai dai ganin ta yi mini tsufa, ta rame,ko ince ma ba tsoka ko ɗaya a jikin fuskar.

Dattijuwar da ta shigo, ta zauna ƙasa tana gaishe mu.

######

[2/25, 16:04] Ummi Tandama😇: *ƘASAITA BOOK 3*

NA

MARYAM KABIR MASHI

Page 8

"Sannu Inna,ban gane ki ba, na so dai in ga kamar na taɓa ganin ki, amma na kasa tunano a ina na taɓa ganin ki."

Sai na ji ta saka kuka tana cewa, "Ai dama na san da wuya ki gane ni Gimbiya ni ce jakadiya."

Kafin ta ƙarasa daga ni har Yarima mun miƙe tsaye tare da kiran Innalillahi wa'inna ilaihir'raji'un! Kamar haɗa baki muka ƙara cewa, "Jakadiya me ya same ki haka?"

"Ai Gimbiya Allah ya yi da ragowar shan ruwana gaba, da tuni da sai dai in kun tunano ni ku ce Allah ya ji ƙaina. Yanzu mu ai mulkin kama karya ake yi mana a Jos, saboda azzalumin Sarkin da aka baiwa sarauta."

"Wa aka ba sarautar?" Yarima ya yi tambayar.

"Wani ne wai shi Abdulrahman, wai ɗan Sarki ne, shi ne yanzu duk abin da ake yi sama da shekara uku duk baku da labari?"

"Ba mu da labari, wajen wa zamu ji?"

"Wajen Mama."

"In ta zo mu bata gaya mana komai. Ni kuma ko na je Jos ba na zuwa ko'ina sai gidanmu,ni kuwa ban taɓa ji ba,mun san dai ance an yi naɗin sarauta a Jos, amma ba mu san me aka naɗa ba."

"Ai abin ba daɗin faɗa,kin gan mu nan jiya muka gudo daga gidan yari. Wahala ta duniya ba wacce ba mu gani ba...." Tasa kuka.

"Ke har da fyaɗe an yi mini, tsofai-tsofai da ni. Ke yanzu dai Allah ya yaye mana masifa kawai."

"Ina su Mansura." Na tambaya cikin sigar tashin hankali.

"Sun gudu su duka waɗanda ki ka sani, maza da mata, saboda kamo su kawai aka dinga yi ana yi masu fyaɗe kullum. Maza kuma a kaiwa shugaban nasu, shi kuma aikinsa kenan amfani da maza. Gimbiya ƙartin mutane ya zo da su sune dogarawansa, sun kai ɗari biyu, ban da ƴan iskan ƴan mata." Ta sake fashewa da kuka.

"Dole ne in neme ku in sanar daku yanda ƙasarku ta koma. Ku yi mana arziƙi ku je ku taimakawa al'ummarku."

"Ina Mai Martaba yake ne ake yin irin wannan abubuwan kafirci?" Yarima ya tambaya.

"Yana nan,ai ya riga ya tsafe shi, sai yanda ya ga damar yi da shi. Waziri da manyan mabiyansa fa an neme su an rasa."

"Innalillahi wa'inna ilaihir'raji'un!” muka haɗa baki.

"Yanzu su waye kusa da Sarki?"

"Wasu ne ya kawo ya zuba masa. Kai bacin su Ahmad fa da ƙila ma an gama da su Mama, to su ke tsaye a kan iyayensu, duk sun ajiye karatunsu, sun zama masu gadin iyayensu."

"Yanzu ke ya aka yi kika gane nan gidan?"

"Gidan su Gimbiya na je na samu maigadinsu, shi ne ya yi min ƙwatancen nan gidan. Shi ya gaya mini ma kuna nan garin, da duk abin da ya faru a baya, saboda mu bamu sani ba. An dai taɓa jin labarin kuna ƴar takun saƙa da Sarki, har na cewa Gimbiya ta tashi tsaye,sa hannu aka yi maku kai da mahaifinka."

"Me ye sa hannu kuma?"

"A je mugayen matsafa su shiga tsakanin masoya biyu."

"Allah ya kiyaye. Yanzu ki tashi kiyi tafiyarki,ni yanzu hankalina a ƙwance ya ke ni da iyalina, saboda haka ba na fatan abin da zai zo ya dagula mini lissafi. Sarauta kuma Allah ya tayashi riƙonta. Amma ni yanzu ko ma sha'awarta ba ma yi, ballantana inji ina sonta."

"Amma Allah ya ja da rai kayi kuskure babba, saboda iyayen ka na cikin bala'i, amma sai ka ce ba ruwanka, yanzu haka fa Sarki ya auri matar nan uwarsu shi wanda aka naɗa, sai fa yanda ta yi da shi. Mama kuwa in zata fita sai dai fa ta fita ta ƙofar nan ɓoyayyiya ta je duk inda zata ta dawo."

"Ban yarda ba, saboda da Mama ta gaya mini. Kin ga tashi ki tafi. Honey ba ta dubu goma ta sha ruwa a hanya, kada ki ƙara dawowa gidana,kina jina?"

"Allah ya ja da...." Ya daka mata tsawa. Nan take na ce, "ya isa. Tashi mu je waje,ki jira ni." Na shiga ɗaki, ita kuma ta tafi waje.

Ina fita na ja ta zuwa bayan gida, na tara masu aikinmu na ja masu kunne a kan kada su sake su faɗa cewar akwai baƙuwa a gidan nan . Na ba ta ɗaki na ɗiba mata sabulu, sannan na bayar a sayo mata kayan sawa.

Satin jakadiya shida kenan a gidanmu, ta yi ƙyau, ta mayar da jikinta tamkar ba ita ba. Yanzu abin da ya rage ƙoƙarin shawo kan Yarima. Jakadiya ta ce mini babu wata hanyar da zamu bi mushawo kan shi illa mu jira zuwan Mama,idan har muka samu Mama ta gaya masa halin da ake ciki baki da baki,wata ƙila ya amince ya tashi tsaye ya nemawa al'ummar da ke ƙarƙashinsa yanci.

Ikon Allah! Yau kuwa safiyar Laraba sai ga Mama ta zo, ganin ta sake lafiya ƙalau kamar yanda take yi mana kenan, ta nuna ba a cikin wata matsala take ba. Dalili ne ma yasa na ɗan tambaye ta ina su Mansura da jakadiya, sai na ji Mama ta ce.

"Lafiyar su ƙalau." Kan ganin bata da niyyar cewa komai yasa na aiki ɗaya daga cikin masu aikina na ce a kira mini baƙuwar nan.

Shigowar jakadiya za ta yi daidai da ɗaga gwangwanin lemon da Mama ta yi. A madadin ta ci gaba da sha, sai aka samu akasin hakan, saboda firgitar da ta yi.

Gaskiya dai ta bayyana daga bakin Mama, wanda Mama har da kukanta take faɗar wasu abubuwan. Hankalin Yarima kam ya tashi. Cikin sakan ɗaya jinin sarautar sa ya gudanyo jikinsa, saboda har wata rawar jiki na ga yana yi. Sai da ya nisa ya kai sau baƙwai, sannan ya miƙe yana cewa.

"Zan je sai na kashe su."

Mama ta yi saurin riƙe shi tare da zaunar da shi, ta koma ta zauna ita ma. Ya dube ta ya ce, "ina nan zuwa da bindigata, sai na kashe shi."

Mama ta yi murmushi, sannan ta yi kirarinsu na manya, shi ne "Ta yaro ƙyau take yi, amma ba ta ƙarko. Ai Yarima duk yanda ka ke tunanin mutanan nan sun riga sun wuce mu. Abin da ya kamata mu yi kawai shi ne mu ma mu dage da roƙon Allah ba dare ba rana. Na farko jakadiya kin fi mu sanin hanyoyin da za'a bi a karyawa Sarki abin da ke jikinsa."

Nan take na ji Yarima ya ce, "Aƙwai wasu addu'o'i da ayoyi ina da su na karya sammu ko wani mugun baki. Ban da ayoyin da Manzon Allah (S.A.W) ya ce mana, tare da koyar da mu yanda zamu aikata su."

Zan sa a yi saukar Alƙur'ani mai girma,sau sittin da baƙwai, wanda kowanne daga ciki za'a tofa a ruwa a yarfawa wanda ake tunanin an yi masa sammu, ba wata hanya da zamu bi illa wannan. Sannan mu duka mu dinga tashi cikin dare muna gabatar da wannan nafilar, da kuma wacce Allah ya hore mana. In zamu iya kuma mu ma muyi sauka da kanmu. Ga addu'o'in da sallar nafila.

Nafila ce raka'a huɗu, kowacce nafila da Ayatul kursiyu ƙafa baƙwai 7, dukkansu bayan ka yi sujjadar ƙarshe sai ka karanta wannan addu'ar. _Wallahu galibun ala amrih,walakin na akasaran nasi la ya'alamun (7),_ Idan mun sallame sai mu karanta wannan addu'ar.

Allahumma wahastu nafsi wa irdilaka sau baƙwai(7), sai mu karanta Laƙada ja'akum, ita ma sau baƙwai(7).

Manzonmu Annabi Muhammad (S.A.W), ya ce wanda yake karanta waɗannan kalmomi guda goma, Allah zai kare shi daga sharri biyar a duniya,biyar a lahira. Ga su nan kamar haka:---

1) Hasbunallahu liddini

2) Hasbunallahu liman ahamman

3) Hasbunallahu liman hasadani

4) Hasbunallahu liman kadani bi su'in.

5) Hasbunallahu indal masala fil ƙabar.

6) Hasbunallahu indal mizan

7) Hasbunallahu indal masala fil ƙabar

8) Hasbunallahu la'ila ha'ildalaihi tawakkaltu wahuwa Rabbul Arshir azim.

Allah yasa mu dace.

Cikakken bayanin maganin sammu,wato yanda za'a bi a karya sihiri,ko wani mugun Aljani mai taurin kai,ko sanin me mutum ya kamata ya yi,mata ko maza. Ana iya neman littafin nan kantin Al'Ameen Bookshop GUZURIN MATA MUSULMAI IZUWA ƊAKIN AURE. Wanda Malam Bashir Aliyu (Bashir) ya wallafa. Za'a samu duk wani ƙarin bayani a ciki.

Cikin wata ɗaya da ƙwana biyu muka gama duk wani tsarin da muke son muyi. Ta hanyar Mama kuma muka samu ta baiwa Mai Martaba maganin da yarfa masa wannan ruwan sauka. Ban da masallatai da Yarima ya dinga bi yana cewa a tayamu roƙon Allah.

Ba na mantawa da duk zuwa Makka da zan yi,wato aikin Hajji,ko Umarah, sai na yi roƙon Allah ya daidaita tsakanin Yarima da Mai Martaba.

Yau ga shi zan iya cewa Allah ya amsa roƙona,dama kuwa faɗa ce ta malamai, cewa duk muminin ƙwarai ba zai ziyarci ɗakin Allah da buƙatunsa ba face Allah ya biya masa buƙatunsa. Sai dai zasu iya ɗaukar yan lokuta, wasu kuma sha yanzu magani yanzu ne. Ko dai ka dawo ka ga alherin abun,ko kuma ma kana can kana dawowa ka samu abin da ka roƙa ya faru.

Mu kanmu ba mu san lokacin da Yarima ya je ga hukumar ƙwantar da tarzoma ta ƙasa ba (Mobile) bayan ya samo taimakon gaggawa, sai dai yau muka wayi gari

muka ji an kama Sarkin ƙarya Abdulrahman da mahaifiyarsa, da Yayarsa Hadiza da duk mabiyansu.

Allahu Akbar! Yau ba wanda bai yi wa Mai Martaba kuka ba, shi da ɗan sa Yarima, wanda suka samu shekara ta biyar ba su ga juna ba.

Gaban bainar jama'a Mai Martaba Sarki Jafar ya rungume ɗansa, wanda ya ɗauki sama da mintuna goma, ya ɗagoshi ya kalle shi, sai kuma ya mayar da shi jikinsa ya ƙwantar. Daga baya ne yake tambayar ina jikansa Ammar. Yaro ɗan shekara biyar da wata huɗu ne kawai babu. Amma har ya zama ɗan saurayi saboda girman jiki da yake da shi.

Bayan ya ganshi ne aka miƙa masa Suhailat. Abin ka ga rashin sani, ta ƙi zuwa wajen Sarki. Da yake Allah yasa ta yi saurin tafiya da gudunta, ta iso wajena ta riƙe ni gam tana nuna mini Mai Martaba.

Hankalin Mai Martaba ya dawo jikinsa sosai, saboda duk ya ruɗe wajen neman su Waziri. To aikin da ya ragewa Yarima kenan, neman dattawan da suka rufa mana asiri da yanzu an hallaka mu. Bayan komai ya lafa ne muka ɗauko hanyar dawowa Kaduna. A hanya ne na ji zazzaɓi ya saukar mini,ga shi ko mun isa gida Yarima ba zama zai yi ba, zai tafi yawon neman su Waziri. Wannan shi ne dalilin da yasa muna isowa Kaduna na ce mu biya asibiti in ga Likita, saboda zazzaɓin da ya rufe ni cikin ƙanƙanin lokaci, wanda ni na san hayaniya ce kawai ta yi mini yawa.

Ina zaune a mota da yara da mai rainonsu a baya. Ni kuwa ina mazaunin kusa da direba, ina jiran in ga inda Yarima zai fito, saboda ba zan iya zirga-zirgar cikin asibitin Arewa Clinic ba. Ganin shi ya taho yana washe baki kamar na yi masa albishir ɗin daɗi, duk da na san yau farin ciki yake. Sai da ya iso ya buɗe mota sannan na ga ya ɗaure fuskarshi.

Ni dai ban ce komai ba, amma ina mamakin ganinsa hannu biyu da wata ƴar farar takarda a hannunsa. Abin da ya sa ban yi magana ba, tunanin ko biyawa za mu yi ƙyamus a siyi magani, amma har muka wuce duk inda za'a samu magani ban ga ya tsaya ba.

Ɗaki na nufa kaina tsaye, saboda yanda nake rawar sanyin zazzaɓi. Ina ƙwance Yarima ya shigo ya zauna kusa da ni.

"Tashi ki karɓi takardunki." Gabana kam ya faɗi, amma na yi saurin tashi na karɓa saboda ganewa idanuwana abin da ke ciki.

Positive (Pregnancy test) . Na ga an rubuta a jikin takardar. Na yi saurin dafe cikina.

"Ciki! Haba." Ya harare ni.

"To me kike nufi?"

"Haba Yarima ciki fa?"

"Kina ko ƙwanto ne?"

"Haba gani na yi duka yaushe na haihu?"

"Ko kina nufin ciki ɗaya ya yi kaɗan? Da gaskiyar ki,ƙato kamar ni a ce ciki ɗaya na yi. Tsaya ki gani in dage in yi na biyu yanzu."

Ya taho da sauri zai hayeni, na yi ɗan hanzarin sauka.

######

[2/25, 21:47] Ummi Tandama😇: *ƘASAITA BOOK 3*

NA

MARYAM KABIR MASHI

"Na tuba wallahi,ɗayan ma ya isa."

"A'a da sauran Waziri da yake gadin ƙofa, tsaya dai ki ga,ke kin ɗauka abin da wasa ne."

Saboda rashin lafiyar da ke jikina yasa na kasa gudu sosai, har sai da ya kamo ni ya ɗauko ni cak, ya ɗora saman gado.

"Yau Celebration (murna) ɗin shiryawa da Mai Martaba zan yi."

Yana magana yana tuɓe rigar yana cillarwa. Ga shi saman cinyoyina zaune,ni kuwa sai dariyar kukan shagwaɓa nake yi, ina haɗa shi da Allah.

Ya yi saurin sumbatar bakina, ya tsotsa, sannan ya ɗago ni ya tattara gashina da ya baje saman gado, ya riƙe da hannu ɗaya.

"Yasmin na gode miki da ki ka taimaka mini da rayuwa mai ƙyau, ingantacciya. Ga shi kina haifa mini ingantattun yara. Na gode Allah da....."

Muryar Ammar ce ta nufo ɗakin mu. Da ji da gudu yake yana kiran.

"Dady ka yi baƙi masu kayan soja, ga su can a get a tsaye."

Cikin gaggawa ya miƙe tsaye yana kokawar mayar da rigarshi jikinsa. Ni kuwa dariyar ƙeta kawai nake daga ƙwance, har Ammar ya shigo, amma riga ta ƙi sanyuwa,dan ma Allah ya taimaka da wandonsa a jikinshi. Ammar na shigowa sai na ji yana cewa.

"Tsaya Daddy kada ka sa rigar."

Yarima ya yi tsaye da riga a hannu.

"Daddy tsugunna ka gani."

Yarima ya tsugunna, Ammar ya taɓa damtsan cinyar hannun Yarima.

"Wai Daddy ka ajiye chuka,ka fita haka,kai ma sojojin su ji tsoron ka,ka bibbige mana su,nima in na girma zan chuka haka."

"Za kayi amma daga yau tsoka ake cewa."

Ya dafa wajen ƙirjinsa,in tuɓe riga in ga ina da wannan."

"Amma ba yanzu za kayi wannan ba, sai kana cin abinci ka girma,ka zama babba kamar ni."

"Mama wai haka?"

"Kai fita ka barwa mutane waje. Ba na hana ka shigowa ɗaki ba sallama ba da irin wannan surutun naka. Fita mana."

Ya juya tare da cewa, "Ki yi haƙuri Mama." Yana fita na taso na ja kunnan Yarima.

"Kai ma ba na hana ka biyewa surutun Ammar ba? Wata rana sai ya baka kunya a gaban jama'a."

"Sorry Mamo." Na ƙara shan kunu na juya. Ya yi saurin fizgo ni jikinsa.

"Sorry Mamo, ina son in na dawo inga an yi mani fara'a."

"To je ka an yi haƙurin, kada a daɗe a zo a bani magani insha."

"Pracetamol ne kawai za ki sha. Bari in ɗauko miki."

"Ni dai gaskiya mai ƙarfi wanda zai hana komai zama cikina."

"Kada ki damu, ba mantawa na yi ba. Kin ga ko Ammar ya ce zan iya faɗa da sojoji,kin ga kuwa ƙyau na ace ciki bibbiyu nake yi." Na ture shi.

"Ni dai je ka."

Ya yi dariya ya saka riga ya fice. Sai da sha ɗaya na dare ta wuce, sannan ya dawo. Da ganinsa kuwa a gajiye yake. Ya zauna kusa da ni cikin cewa.

"Wash!"

"Sannu."

"Ke dai bari wallahi, na gaji sosai, ta so muje ɗaki,dama dai ni ake jira, bari in ɗan watsa ruwa in ji sanyi."

"Abincin fa?"

"Zan ci, bari dai in samu kaina tukunna."

Bayan ya fito ne yake ba ni labarin cewa wajen su Sarkin ƙarya Abdulrahman ya je, saboda yasa a tuhume shi inda ya kai su Waziri. Da ƙyar ya faɗa, shi ma gani ya yi za'a kashe shi a banza. Kin san inda ya kai su?" Na girgiza kai, tare da matsowa irin na mai ɗokin a gaya masa.

"Suna babban gidan yarin Legos,ƙiri-ƙiri Prison."

"To ya za'ayi yanzu?"

"Sai gobe zamu je mu taho da su. Kai Allah dai ya kusan raba mu da ƙajaga."

Haka dai muka dinga tattaunawa har muka ƙwanta.

N.T.A Kaduna, gidan talabijin na ƙasa, shi muke kallo. Inda muka ga su Yarima na saukowa daga jirgi da su Waziri a bayanshi, sun kai su talatin, dukkansu kamar za su kife ƙasa saboda rama, ga tsufa,ko kuwa in ce yunwa. Amma kaya ne masu ƙyau a jikinsu, ga shi sun sha aski. Jakadiya kuwa, sai kuka take yi,wai tunanin wahalar da ta sha take yi.

**** **** **** **

Wata ɗaya kenan da sati uku da dawowar su Waziri wanda ya yi daidai da yau aka yankewa su Abdulrahman da Yayarsa Hadiza da uwarsu Asabe da sauran muƙarrabansu hukunci a babbar kotu ta jaha, wacce ta yanke masu hukuncin ɗaurin rai da rai, saboda bincike ya nuna Abdulrahman da mabiyansa an kama su da laifin fyaɗe, aikata aikin alfasha da maza, shaye-shaye,kisan kai. Ga shi dama wai sana'ar shi fashi da makami.

Hajiya Asabe uwarsu kuwa an kamata da laifin yin zina kafin ta yi aure, da ta yi kuma tana shigo da wani namiji a cikin gida. Tuhumar ƙarshe kuma ta tabbatar cewa su Abdulrahman ba yaƴan Sarki ba ne, sakamakon faɗi da tayi da bakinta cewa yaƴan faranta ne.

Hadiza kuwa zaman kanta take yi yanzu haka, ban da gidanta ne matattarar yaƴan duniya, ban da bin bokaye da take yi, wanda ya bayar da tabbacin har maƙabarta an taɓa kama ta tana tono wani sashi na jikin matacce. Wa'iyazubillah. Allah ka cikamu da imanin mu,masu yi Allah ya shirye su. Na faɗa a zuciyata.

An yi an gama, sai rigima ta dawo kan Yarima, wanda aka zaɓa a matsayin shi zai hau kujerar sarauta, amma ya ƙiya, ya ce shi da Jos har abada. Wannan al'amari ba ƙaramin tayar da hankalin jama'a ya yi ba. Har ya zama garin Kaduna yaƴan garin sun zo, tunda kullum ma samu baƙi yaƴan baiwa Yarima haƙuri, da ba shi baki akan ya koma gida. Amma maganar shi ɗaya ce Kaduna ta yi masa, shi hankalin shi a ƙwance yake.

Yau kuwa manyan baƙi ne, wato ƙungiyar su Waziri, amma Yarima ya ƙiya. Da na je gaishe su suka dinga roƙona a kan in ja hankalinsa in nuna masa muhimmancin mutanen da zasu zauna a ƙarƙashinsa. Na bisu da to. Amma na san ba zan iya tunkarar Yarima da wannan maganar ba.

Su Daddyna sun zo tare da Mamee, amma sai ya ce masu insha Allahu zai yi,su bashi lokacin ya yi tunani. Haka suka tafi suna murna. Amma suna tafiya ya ce ai shi sam,kunyar su tasa ya amsa masu. To ni kuwa dama da na ɗauko hanyar yi masa maganar, kallo ɗaya yake yi mani in yi shiru. Wani lokacin ma har in samu la'adar cewa ba ni da hankali.

Sarki Jafar Sada ne yau da kanshi da Iyalansa gaba ɗaya a gidan mu,Mama, Hajiya Kilishi, Ahmad,Yaya Salimat,Sauda, da Idris,Sarki ya yi gyaran muryar da dukkanmu sai da muka nutsu, sannan ya soma magana.

"Faysal my lovely son. Da farko zan fara da roƙon Allah ya raya maka zuri'arka, ya yi maka sakayya da aljannar fiddausi.

Faysal,sanin kanka ne ba mai raba ni da kai sai Allah, amma akasi ya faru tsakaninmu ta sanadiyyar yaudara da aka fara yi ta hanyar gaya mana aibunka da illolinka. Ban yarda ba da farko, sai da aka kawo mini shaida ta zahiri."

Ya buɗe wata ambulan ya miƙawa Yarima kaset da wasu hotuna.

"Duba!" Ya ajiye.

Ban kawowa raina komai ba. Ta haka ta fara yaudara ta. Ganin raina ya ɓaci matuƙa har na ɗan yi fushin ƙwanaki da kai,ai sai wannan hanyar ta ba shi damar shigo da abubuwan da na san sun daɗe yana tanadar su. Magana dai ni ke son ta wuce,a taƙaice ina neman a yi haƙuri a kan duk abubuwan da suka wuce,a taryi gaba,a kiyaye. Ko kana da magana?"

"Baba ni ban ce kayi mini laifi ba,ni ban riƙe kowa ba,ni dai nayi kokawar ƙwato maku yanci ne don kuna iyayena, amma ba don na hau gadon mulki ba. Na gode ƙwarai da ƙyautar da ka yi mini da nuna ƙauna, amma na barwa ɗaya daga cikin ƙannena,ai su ma sun girma. Amma ni Kaduna zan cigaba da zama, saboda hanyoyin cin....."

Ya miƙe ya je ya tsugunna ya kai gaisuwa. "Amma idan na ɓata muku rai ku gafarce ni." Ya miƙe ya shiga ciki.

Falon mu ya yi shiru har tsayin mintuna masu tsayi. Can Sarki ya nisa, "Yasmin, Hajiya Mariya, Hajiya Kilishi, aikin ku ne,kushawo kan ɗanku. Ke kuma mijinki. Koma in ce aikin ki ne. Yasmin ki taimaka ki shawo mana kan mijinki, ya taimaki jama'ar da ba mu san iyakacinta ba."

Ba ni da damar yin gardama, sai dai na bishi da, "To Baba, za'ayi ƙoƙari."

Ni kuwa har hantar cikina sai da ta kaɗa. Daga nan kuwa aka cigaba da yɾar hira, jin falon ya kaure da surutu yasa Yarima ya shigo shi ma ya zauna aka ci gaba da yi dashi.

Sai da suka ci abincin ranar mu, sannan suka tafi,mu kuwa rakiya har mota. Yau an samu shiga, bayan mun dawo hirar mu kawai muka cigaba har ya tafi gona.

Bayan mun shiga ɗaki ne har ma mun yi niyyar ƙwanciya kenan an gama duk wata hira. Na ɗauko Novelle Gelly ina shafawa a jikina, domin jikina ya ɗau ƙamshi gaba ɗayan shi. Gefen gado na zauna, amma gabana ke ta wani irin mummunan faɗuwa, saboda maganar da nake son ta fito daga bakina. Ban kashe fitila ba na hayo gado na zauna kusa da shi tare da robar man ƙamshin jikin nan a hannuna,sai kuwa kaɗawa take yi, da alama jikina ke rawa.

Sai da na karanta addu'a sannan na ambaci sunan shi.

_Ya waliyyan ni'imati,wa mallazi inda kurbati,ij'alni matahu bardan wasalam alayya kama ja'altana barda wassalamun ala Ibrahim (Ƙafa baƙwai).

"Honey." Na kira shi a sanyaye.

"Ina jin ki Sweetyna." Ya faɗa, har da ɗora hannunsa a saman cinyata.

"Magana nake son mu yi da kai mai mahimmanci."

"Ina jin ki. In kuma so ake in ƙara wani cikin, to ban manta ba." Ya faɗa har da ɗan taɓa mini gefen cikina. Na yi murmushin da yake haɗe da fargaba.

"Honey maganar sarau...." Wata tsawa da ya daka mini. Bani ba,na yi imani maigadi ma ya tsorata. Ni kuwa har na kai bakin gado, saboda na yi zaton duka ne zai biyo baya. Tun kuwa da na sauka, na durƙushe nake jin ɗan cikina na mutsulniya, tamkar ɗan kifi a ruwa.

Bai ƙara cewa ƙala ba daga wannan, sai ma ya juya min baya. Gaskiya na san na yi awa ɗaya durƙushen nan, ina saƙa hanyoyin da zan bi. Ganin ba shi da wani alamun motsi ballantana in san hanyar da zan bi, sai na ce, "Wash! Wash!! Wash!!! Cikina." Ina faɗar cikina na ga ya yi saurin saukowa.

Tun daga can na ji yana cewa, "Me ya samu cikin? Da ke nake,me ya samu cikin?"

"Ciwo yake. Marata!"

"Tashi mu gani."

Ya yi saurin isowa ya kama ni. Na lanƙwashe.

"Ba zan iya ba, ina jin ɓari zan yi."

"What? To kin ga ni ga irin ta nan,kin sawa ranki abin da ba ruwanki, ga shi nan za ki janyo mana asarar yʻayʻana. Taso mana mu tafi asibiti." Ya sake ni, ya tafi ya buɗe durowa ya ƙwaso mana kaya. Ya zo ya kama ni.

"Tashi, sannu." Ya yi alamar ɗaga ni. Na riƙe hannunsa.

"Yarima!”

"Ba na ce bana son kina kirana da wannan sunan ba?"

"Na sani,ka yi haƙuri, amma yau ne na ƙarshe, tunda ka nuna mini ba ni da amfanin komai a wajen ka. Yau zan haƙura da auranka,gara ka auro wacce take da muhimmanci da amfani a wajenka." Sannan nasa kuka.

Ina jin sa ya tsugunno. "Yasmin me ya faru? Me na yi miki? Ba ki taɓa gaya mini magana mai ɗaci ba sai yau."

"Yau ma kamawa ta yi." Ya ɗago kumatuna.

"Haba Yasmin, ya zaki tayar da hankalin mijinki...."

"Ba ka son a tayar da hankalin ka, amma kai zaka tayar da na mahaifinka?"

"Ba ruwan ki da maganar mu."

"Kenan ba ruwan ka da ni? Don Allah in tambaye ka?"

"Ina jin ki."

"Yanzu me ye nan cikina?"

"Ɗana ne."

"Kana son shi ko baka so?"

######

[2/28, 08:27] Ummi Tandama😇: *ƘASAITA BOOK 3*

NA

MARYAM KABIR MASHI

Page 10

"Wacce irin magana ce wannan Yasmin?"

"Ka ce mini eh ko a'a."

"Ina son shi mana."

"In ya zube za ka ji ciwo."

"Ƙwarai kuwa."

"To ka yi tunanin irin ciwon da za ka ji,ka ƙwatanta shi ga in ka rasa ɗan da ya girma za ka ji ciwo. To mahaifinka abin da yake ji a zuciyarshi ya linka naka dubu,

kuma tunda ba ka jin ban haƙurin shi, to ni ma ba zan ji ban haƙurin ka ba, zan bar maka gidanka da yƴayƴanka, amma zan tafi da cikin jikina,in je Likita ya cire mini...."

"Ki rufa mini asiri Yasmin,duk wata taƙamata taki ce,kin zauna da ni a lokacin da na shiga babban tashin hankali, sai kuma yanzu a kan ƙanƙanin abu ki ce ba zaki zauna da ni ba."

"Kai ka ɗauke shi ƙarami."

"Yasmin ke nake ji, ina son ki,ina son zama da ke, muddin na karɓi sarautar nan sai ya zamo na yi miki amarya."

Ɗan cikina ya sake wajen ƙwanciya da saurin gaske, saboda tashin hankalin da maganar Yarima ta haifar. Jinyar sakan biyar na yi sannan na yi magana.

"Na amince ka yi idan dai har za ka bi maganar iyayenka."

"Yasmin kin kuwa ji abin da na faɗa?"

"Na ji, cewa ka yi zakayi min amarya,ko ba haka ka faɗa ba?"

"Haka na faɗa,kin amince?"

"Eh, amma kai ma in ka amince gobe da safe za mu je Jos,ka gayawa Sarki ka amince da abin da yake so, sannan za ka koma Jos da zama,in ba haka ba,yau ba zan ƙwana gidan ka ba."

"Wannan ma bata taso ba,dama na ga wata yarinya ɗazun da na dawo daga lambu, sai kallona take yi,kin ga shi kenan sai in koma in gani. "Yƴar gayu ce."

Na yi murmushi, "Kyan Namiji dama ya auri mace wacce ya gani da idonsa ya ji ta ƙwanta masa a zuciya, ba wai wani ya gane masa ba."

"Yasmin kenan, ba ki san cewa matar daraja da ɗaukaka ta bi bayan zaɓin Iyaye....."

"Ya isa,mu je mu ƙwanta."

"Cikin fa?"

"Ya lafa, zan iya kai wa safe." Ya kama ni muka je muka ƙwanta.

**** **** **** **

Taro kan ya haɗo jama'a, ta ko'ina, sai isowa suke yi. Manyan sarakuna na ƙasa, gwamnoni,kai har da shugabannin kasashe, duk sun iso filin jirgi na garin Jos. Mu kuwa muna gefen mata, wajen su Mama, amma ni ma da tawa gayyar a bayana.

Yarima na can daga sashen su Mai Martaba ya sha alkyabbar alfarma. Abin ka ga farin mutum, ya yi ƙyau, wanda ba ya misaltuwa. Ni kuwa ni da Aunty Salwa daga ni sai ita muna hirar jama'ar da ke wucewa.

Bayan kamar awa biyu kowa ya gama zama aka ce Sarkin Malaman Sarakuna ya zo ya buɗe filin taro da addu'a (Adalin Sarki kenan,Sarkin Musulmai Dr. Usman Nagwaggo) Sarkin Katsina kenan. Dattijo fari tas, mai ruwan matasan yara, jikinsa ba ya tsufa. Shi ya fito ya fara jero addu'o'in buɗe taro tamkar wanda ya girma a tsakiyar Larabawa, saboda harshen da ya karya tamkar na matashin Balarabe.

Tsayawa bayanin abubuwan da aka yi ma mun san ɓatawa kanmu lokaci ne, balle lissafa manyan da suka halarta. Amma mun san Sarkin Sarakuna na Nijeriya, manya ba wani a gabanka, shi ya yi naɗin sarautar,wato Mai Martaba Alhaji.Dr. Ado Bayero, wanda jama'a ke so kenan.

**** **** ****

Wani irin mahaukacin gida ne aka bai wa Yarima, har sai da ya ba ni tsoro. Na kalli gidan, daga ni sai ƴayƴana biyu, sai cikin da ke jikina wanda bai wuce wata baƙwai ba. Masu yi mana hidima kuwa ba su ƙirguwa, amma Mama ta ce in dinga yi wa mijina abinci da kaina. Haka kuwa aka yi, duk na ware ɗaki ɗaya na mayar da shi kicin ɗin kaina, wanda ni kaɗai ke shigarsa, sai kuwa ƴayƴana, amma ko jakadiya shakkun shigarta ciki nake yi.

Tsarin kundin littafin mulkin aka damƙawa Yarima domin ya yi nazarinsa, duk da ba wai shi kenan Mai Martaba ya daina aiki ba, a'a mulkin na ga hannun Mai Martaba, Yarima kamar ɗalibi ne da malami, wato ya koyi yanda ake yi, tun kafin Mai Martaba ya rasu ko kuwa ya yi tsufan da ko ya yi magana ma jama'arsa ba za su saurare shi ba,ko kuwa a dinga cewa ruɗin tsufa ne, amma yanzu da hankalinsa, duk abin da aka yi ba daidai ba zai tsawatar.

Dama su tsarin mulkinsu kenan, shi ne a baiwa wanda ake ganin ya cancanta a baiwa sarauta, tun Sarki na da rai, ba don komai ba sai don ya ga yanda zai tafiyar da nashi tsarin mulkin, saboda in ya yi kuskure a nuna masa hanyar gyara.

Shi kuwa Yarima, sabon tsari muka zauna muka gyarawa littafin nan, saboda wani al'amarin da ake yi yakan ɗan taɓa talakawa, sannan shi Addininmu ya nuna za'a tambayi duk wani mai mulki haƙƙin yanda ya tafiyar da talakawansa.

*** *** *** ***

Tsarin da Mai Martaba na biyu ya yi, ya burge kowa, ya kuma ƙara masa farin jini a wajen talakawansa. Tsarin kuwa shi ne da kansa ya zagaya garin Jos da kewayenta

domin sanin halin da talakawansa ke ciki. Wasu lokutan kuwa ma ba a shigowa a mota sai a ƙafa, wasu kuwa ƙwatami ya yi yawa, wasu ƙauyukan kuma da ƙafa ake zuwansu.

Wannan rangadi ya ɗauke shi tsayin wata biyu har da ƙwanaki goma sha baƙwai,yana yin shi. Wata rana Yarima ya dawo da fara'a, wata rana kuwa da kuka yake iso mini,saboda irin ganin da idonsa ya yi na halin da talakawansa ke ciki.

Ni kuwa ciki ya tsufa, amma har yanzu haihuwa ta ƙi zuwa, wanda zan iya cewa na shanye watan haihuwata, ma'ana na wuce watan haihuwata. Wannan kuwa ya tayar da hankalin Mai Martaba na biyu, Yarima kenan.

Ƙarfe tara na dare shi ne ƙa'idar tashin Yarima daga fada, saboda ya samu lokacin hira da iyalinsa. Yau ma kuwa haka ya shigo gida, ya sameni ƙwance a ƙasan kafet ɗin da kusan launinsu ɗaya da katifa. Suhailat na ƙwance a gabana ta yi bacci. Yanayin yanda fuskarsa ta nuna shine yana tausaya mini. Yana isowa ya sunkuya ya ɗauki Suhailat ya kai ta ɗakinsu, sannan ya dawo ya durƙusa a gabana. Ya sunkuya ya sumbaci kumatuna.

"Sannu." Na ɗan yi fari da idanuwana

"Wallahi Yasmin ina tausaya miki."

*Ni kuma kai nake tausayawa, saboda aikin da ke gabanka na jagorantar mu. Ga ni da yayanka,iyayenka da nawa,ga jama'ar garin. Ga jama'ar garin nan ba ki ɗaya duk fa a ƙarƙashin ka muke. Yanzu in mutuwa ta kama ka ka ce da Allah me?"

"Wallahi kuwa,ai shi yasa nake son in ga kin haihu lafiya sai mu zauna mu yi shawarar ya zamu yi balle dama duk inda muka je an ɗaukar min shi a kaset, sai mu sa a tsanake mu ƙara gani."

"Honey,tunda haihuwar ta ƙi zuwa me zai hana a fara, tun da idona da bakina za su yi aikin ba cikina ba. Yanzu da ka ce a bari sai na haihu,to in na mutu wajen haihuwar fa..."

"Haba Yasmin ki daina irin wannan mummunar maganar ta ƙananan yara,me ki ke so na koma idan na rasa ki?"

"Baka zama komai."

"Na ji nidai ba na son ki dinga yi mini irin waɗannan maganganun marasa daɗi da ɗaci."

Ya juya har da ɓata rai sosai. Hannu na sa na juyo fuskarsa.

"Sorry, ba zan kuma ba na daina." Na faɗa cikin muryar nadama.

Ya ɗago fuskata ya ƙura mini ido, sai kawai na ga ya kai bakinsa ga nawa. Mun yi minti huɗu ya ɗago.

"Yasmin ni fa har yanzu son ki bai taɓa raguwa a zuciyata ba,kin san Allah duk every day, every time, every minute,every second,sai na ji sonki yana ƙaruwa a zuciyata. Ki daina gaya mini maganar da raina zai ɓaci,ki tayarwa da mijinki hankali,kin ji?" Na ɗaga kai alamar eh.

"To bari na ɗauko kaset ɗaya mu fara da shi."

Na yunƙura zan tashi ya yi saurin kama ni, na miƙe.

"Ina za ki?"

"Da abin hira zan ɗauko maka,in samu kuma in cire maka kayan jikinka."

Ya ja kunnena, har sai da na yi yʻar ƙara.

"Ke ɗin nan ba ki jin magana,sau nawa ina gaya miki cewa idan ina cikin gida kusa da ke na zama ɗan aiken ki.?"

Na narke na yi irin alamar kukan shagwaɓa, tare da maganar shagwaɓa.

"Ni Allah ban yarda ba,ni sai in dinga baka wahala."

"Wallahi na cije bakinki idan ya ƙara yi mini gardama."

"Ni! Ni! Dai...." Ya zare takalman ƙafarsa zai ƙwala mini cikin haushi. Na yi gaba da ɗan guduna, ina kiran.

"Na daina, na daina, Allah....."

Ya kamo ni saboda irin yanayin gudun mai ciki. Ya ɗaga takalman, na runtse idanuwana alamar tsoro, sai na ji ya zagayo ta bayana ya rungume ni yana dariya.

"Ga tsoro ga jan faɗa."

Dama yanda yake rungume ni kenan idan ina da tsohon cikin da zai hana masa sakewa ya rungume ni ta gaba. Ya sumbaci wuyana.

"To mu je in taya ki ɗaukowa."

"To tsaya in cire maka alkyabbar ko?"

Ya juya baya na zare masa alkyabbar jikinsa na ajiye saman kujera, sannan muka isa kicin.

Ba wani abu ba ne mai wahala ba abin hirar tamu. Tuwan abarba ne da inibi,an markaɗe su da ɗan kauri, tare da dabino wanda za'a jiƙa shi ya yi laushi, sai a ajiye ruwan gefe ɗaya, sannan a samu ƙwaƙwa ta ciki a goga ta da abin goga kuɓewa, bayan duk an wanke su kenan, sai a kawo ruwan abarbar da dabino da inibi a zuba a cikin ƙwaƙwar, sai a kawo madarar ruwa a zuba a ciki, ya danganta da yawansa, yawan madarar ga mai son suga ya zuba, ga mai son zaƙi sosai zai ji ya yi daidai. Amma ko ba inibi za'a iya yi, ana iya yi da madarar gari ma.

Cikin ɗan kofunan shan fruit salad ake shan shi, tare da ɗan ƙaramin cokali ana kiranshi da suna Appitizier (Coconut).

Mun kalli kasusuwan da dama a cikin ƙwara tara,babu abin da na lura a ciki wanda yake takurawa talakawa illa abubuwa baƙwai. Abin da muka zauna a yau juma'a muna tattaunawa da Yarima kenan.

"To ke yanzu me kika lura ya damu talakawana?"

"Ai ba talakawanka kaɗai ba, duk yan ƙasar Nijeriya."

To yanzu kamar me ye da meye ki ka lura da su?"

"Ruwa, rashin abin ƙonawa, itace ko kalanzir,ko gas,ga masu aiki da shi, ba wai babu ba, tsada ce ta yi masa yawa, suna buƙatar magudanan ruwa,takin noma, magunguna a asibitoci, hanyoyin mota, ballantana a cikin ƙauyuka, wutar lantarki,makarantun boko, Islamiyya tare da ilimintatun malamai,uwa-uba fetirin sawa motoci ko abin hawa ƙanana.

"Gaskiya na yarda. Ke kin ga wani ƙauye da muka je,kin ga ruwan da suke sha kuwa tamkar ruwan ƙwatami? To wai me ki ka ga ya janyo haka?"

"Rashin kulawa da sa ido, da zame hannu da ku sarakuna ku ka yi,ku ka bar wa gwamnati komai, ita zatayi. Ka yi tunani lokacin da sarakuna ke mulkin garuruwansu ka gani,ka san ya sha bamban da yanzu. A da Sarki ke da ikon komai kuma yana samun hanyoyin jin labarin abin da talakawansa ke ciki ta hanyar fadawansa da kuma yʻan garin kansu. Ka tuna a da ko haihuwa aka yi a gari sai Sarki ya sani,ko hakimi,ko Dagaci,ko Mai unguwa, amma yanzu fa? Kai za ka baiwa kanka amsa."

"To yanzu wacce shawara za ki bani?"

"Ni dai shawarata biyar ce. Ta farko itace sarakunan mu su yi haƙuri don girman Allah su dawo da yanayin mulkin su na da, da adalci,su tuna su zasu fi sanin gwamna ko shugaban ƙasa, abin da talakawa ke ciki, saboda sun fi su hulɗa da jama'a,su manta da duk wani abin da aka yi masu,su ji tsoron Allah,su kawar da komai da ke zuciyarsu,su ci gaba da aikata ayyukansu na alheri, kamar yanda ake yi a baya.

######

[3/1, 19:48] Ummi Tandama😇: *ƘASAITA BOOK 3*

NA

MARYAM KABIR MASHI

Su yi tunani da cewa Allah Subhanahu wata'ala ya damƙa ragamar mu a hannunsu, duk da na san yanzu haka in baku sarakuna ba yanda za'ayi gwamnati ta tafiya, duk da na san a kan san rai ne da ɗan nuna maku isa, amma kamata ya yi ku dage da ƙwarjinin da Allah ya ba ku ku nunawa Gwamnati dole sai daku za ta iya tafiya. Lallai wannan babban jihadi ne ga rayuwar duk wani mai faɗa aji a duniyar mu ta musulunci.

Saboda la'akari da abin da malamai suke faɗa cewa, ranar ƙiyama ana fara hisabi ta jini ne, sannan kuma manyan malamai, masu kuɗi, shugabanni, sarakuna, saboda haka wannan ma ya ishe mu ishara ta mu dage mu ga yanda yɗan ƙasa mu suke tafiyar da rayuwarsu, saboda shi Allah ba ruwansa gaba ɗaya zai haɗa mu ya tambaye mu yanda muka tafiyar da mulkinsu, ba ruwanshi da cewa shugaban ƙasa ko gwamna, mulki duk mulki ne.

Ko mace a gidan mijinta ita ma mulki take, haka namiji a tsakiyar iyalinsa duk mulki yake. Za'a kuma yi masa hisabi a ranar gobe ta yaya ya tafiyar da iyalin nan nasa kamar yanda muka sani, ga hadisin Manzon Allah (S.A.W) da wasu daga cikin ayoyin Alkur'ani mai girma.

Lallai waɗannan hadisai ana iya duba su ga litattafan Buhari da sauran sahihan litattafai. Ku sani talakawa na cikin masifa kala-kala, waɗanda suke neman taimakon Allah, tare da shuwagabanninmu. Lallai Allah yana sane da duk wanda ya taimaki wani, ya ƙyautata rayuwarsu ta zamo ingantacciya. Allah ya taimaka maku, shiyasa nake tausaya maka.

A saboda haka fushi da sa ido ga shuwagabanninmu ba na sarakuna ba ne, ba haƙuri da tausayawa talakawansu shi ne nasu, da hanyoyin da za su bi su ga sun gyara, sun dawo mana da jin daɗin da ya wuce, wanda muke tunanin ba zai taɓa dawowa ba,su yi mana bazata su dawo mana da shi. Allah ya taimake ku, ya sada ku da gidan Aljannar fiddausi madauwamiya, Allah ya raya maku zuri'arku, ya ƙara taimaka muku da haƙuri da mu,Amin."

"To yanzu wacce shawara za ki ba ni?"

"Shawarata a nan ita ce,ka fara yin amfani da abin da ke hannunka, ikon mallakar ka."

"Kamar me?"

"Kamar ɓangaren abinci. Ka ga yanzu haka a gidan nan zuwa gidan da muka baro, zuwa gidan Mai Martaba na ɗaya,aƙwai ɗakunan ajiyar abinci sun kai talatin (Stores), kowanne da kala-kalar abin da ke ciki,na yi imani in zamu shekara ɗari ba zamu nemi abinci ba, amma ka sani shi abinci ne ba zai kai shekara ɗari ba, da kuma mu da koyaushe Allah zai iya ɗaukar ran mu, sannan ko da yaushe abincin nan na iya lalacewa.

To me zai hana a taimakawa talakawa da shi, sannan kuma Allah ya hore maka maƙudan kuɗi, ba Mai Martaba na ɗaya ba, ba kai ba,ni kaina da nazo gidanka daga baya, na san na mallaki duniyoyin da zan iya taimakawa da su daidai gwargwado."

"Ai kuwa na gode, Allah ya yi miki albarka, ya baki yaya masu ƙaunar ki kamar yanda ki ke ƙaunar ubansu. Da kin haihu kuma zan fara."

"A'a ba ruwanka da haihuwata,ka cigaba kawai."

"Ai saboda matsalar mata sai ke."

"Ga jakadiya nan na amince da ita,ka yi tunanin ƙaunar da take yi mana, iyaka ni zan dinga tsara mata abin da ya kamata ta yi, ba ma sai na fita ba."

"Ni dama ai ba na son ki fita a gane mini ke,kin manta ke One in town ce?"

"Wallah Honey ka bar koɗa ni zanyi maka kuka."

"Na daina,ai ba na son inyi asarar hawayen nan naki masu ɗigon tawwadar ilimantarwa."

"Ka ƙarayi."

"Sorry My Beby na."

Na yi dariyar jin daɗi, tare da juya bayana na ƙwanta a ƙirjinsa, ya rungume ni.

Na godewa Allah da ya wadata ni da miji mai jin shawarata, mai ɗaukar duk kalamain da ya fito daga bakina,ko na iyayena. Wannan dalili ne ma yasa na sadaukar masa da nafila raka'a biyu domin ta zama kariya a gare shi, wacce nake zama musamman in yi masa ita shi ɗaya, da addu'o'in da ke cikinta.

Dalilina kuwa, shi ne duk abin da muka tattauna da Yarima ya aikata shi, duk unguwa idan suka isa, tun daga gidan farko har ƙarshe sai an ajiye masu buhun-hunan abinci da jarin sana'a, wanda na tabbatar zai wadace su. Sannan sai a tambayi matsalar ka ta rashin lafiya ko haihuwa,ko bikin ɗiya,ko gyaran gida, sai a taimaka maka.

Wasu buhun-hunan abincin kuwa, don ajiya har sun lalace da hunhuna, sai waɗanda ƙwari suka cinye suka koma gari. Kai Alhamdulillahi, saboda yanzu ni na san nayi jihadi mai tsananin lada, tun da har Islamiyoyi aka buɗe, ban da makarantu masu ƙyau, ban da ɗaukar nauyin yaƴan da iyayensu ba su da halinsa su makaranta.

Sai kuma ni tawa gudunmawar, shi ne taimakawa mata yan'uwana da koyar da su ilimin zamani da na addini, yanda za su zauna da mazajensu lafiya da tarbiyyar yaƴansu, ga sana'o'i ana koya masu. Abin da ya so ya bamu wahala ni da Mai Martaba na biyu, shi ne Musluntar da arnan da suke zagaye da Jos, waɗanda wasun su ko kaya ba su iya sakawa ba,wasun su ma nama danye suke ci, amma mun samu da ƙyar mun taimaka masu.

Dabarar da muka yi kuwa, shi ne duk garin da suka isa, sai su ɗauko shugabansu su taho da shi cikin gari ya samu wata ɗaya,ko biyu yana ganin yanda jama'a ke rayuwarsu, ana koya masa duk wata al'ada mai ƙyau da Addininmu, to idan ya koma garinsu, shi zai dinga koyar da yan'uwansa,idan ya ga suna da sha'awa sai ya dawo gari ya gayawa Yarima, daga nan sai a tayar da mutane kamar ashirin cikin su da malamai da masu taimaka masu da abinci, ruwan sha,wanki. Yanzu haka duk an tura su a matsayin zasu shekara a can.

**** *** ****

Cikin jikina dai har ya shiga wata na sha ɗaya a jikina babu zancen wata haihuwa, sai dai duk inda na zauna sai an taimaka mini nake tashi,don dai ma ni doguwar macece, da gajeriya ce da shi kenan sai an dinga saka ni a kujera ana turawa. Wannan abin yanzu shi ya damu duk wani masoyina.

Kai har da Mai Martaba Sarki ya aiko da cewa mu shirya zai turo likitocin da zasu duba ni. Shi kuwa Mai Martaba Yarima cewa yake gara mu bar ƙasar. Amma Sarki ya hana a je ko'ina ya ce saboda abin da tafiyar mu zata haifar, shi ne a shiga ruɗanin ya ya nake. Ni kuwa har mamaki suke ba ni, saboda ba na jin ciwon komai sai dai nauyin da cikin ya yi mini ya hana mini sakewa.

Likitoci turawa mata,su baƙwai suka iso gidanmu, ba wani ɗan rakiya sai Mai Martaba na ɗaya, yanda suka shigo falon ina tule waje ɗaya, shi ya bani kunya. Cikin matsananciyar kunya na samu na gaida su, daga nan kuwa suka umarce ni da in isa asibitin mu da ke cikin gidanmu.

Yarima kuwa kamar ya saka kuka, da ya ga likitocin nan, sai dai ganinsu tare da Mai Martaba yasa ya kasa yin magana.

Lallai na san an shiga ɗakin asibiti da ni, ɓangaren mu wato Emir's section.

**** *** ****

_Innalillahi wa'inna ilaihir'raji'un!” haka Mai Martaba yake faɗa yayin da yake riƙe da ɗansa Yarima, wanda ke zaune dirshan a ƙasa yana kukan mutuwar matarsa Yasmin. Wanda hakan ya faru ne ta sanadiyyar haihuwa da ta zo mata da gardama.

Babanta Alhaji Sani Sa'id shi ne ke da ƙarfin halin yiwa mijinta nasiha.

"Haba Yarima,ka yi haƙuri mana,ka yi tunani da Allah ne ya baka Yasmin,don ya ɗauke abin shi kuwa,ai ba a ƙi gode masa ba. Mu ma nan fa jiran tamu mutuwar mukeyi, saboda faɗar Allah Subhanahu wata'ala ce da yake cewa KULLI NAFSIN ZA'IKATUL MAUTI (Dukkan mai rai mamaci ne). Saboda haka ƙyau a ce godiya ga Allah ka yi, tare da yi mata addu'a.

Wannan nasiha ita ta ƙarasa rikita Yarima, sai dai aka ganshi zube a ƙasa sumamme,gudun kada hankalin jama'a ya tashi, yasa ba'a yi wata hayaniya da ƙarfi ba, sai dai ɗauke shi aka yi aka kai shi asibiti, wanda likitoci suka bi bayansa.

Maganar da na yi ita ta dawo da hankalin jama'a gareni, wanda ɗakin cike yake da mata yan'uwana. Cikin su kuwa har da Mamee, Aunty Salwa,ga Mama,da Hajiya Kilishi, ban da jakadiya da ke rakuɓe a gefe, duk na karanci hakan kafin na kai ga yin magana.

Maganar kuwa ta yi daidai da firgita duk wanda ke zaune, ganin yanda suka nuna.

"Mamee lafiya na ga kuna kuka?"

Tambayar da na yi masu kenan. Gaba ɗayansu sun firgita, wanda dukkansu sun yo kaina, kowa so yake ya rungume ni. Jin jakadiya ta fita da gudu tana kira, "Mai girma Yarima Gimbiya ba ta mutu ba,dogon suma ne."

Maganar ta ta iso a kunnena, ita ta gaya mini da jira ake gari ya waye a kaini kabarina.

Na yiwa Allah godiya da ya taimaka mini na farka kafin gari ya waye. Na yunƙura zan tashi, amma na ji jikina kamar an karya mini ƙafafuna. Sai dai ji na yi Hajiya Kilishi na cewa.

"Jira a taimaka miki. Ke kuwa ai dole jikinki ya yi tsami,a haihu tun safe amma ba wanka." Sai a lokacin na faɗa tunanin abin da ya faru da safiyar yau.

Zuwan likitoci da Mai Martaba Sarki, wanda suka yi mini wasu allurori sun kai biyar. Yarima har faɗa yake masu, shi kuwa yana tallabe da kaina a cinyar shi yana yi mini sannu, balle da na ji wani bala'in ciwo na jijjiga mini tsokar naman jikina. Ban fi mintuna arba'in ba a haka sai na ji kamar an zare numfashin jikina.

Daga nan ne ban ƙara sanin yanda aka yi ba, sai yanzu, amma na ji Yarima na yi masu faɗa. A can cikin tsakiyar kaina ina jin matsanancin ciwon da nake ji, sai na ji suna ce masa wai allurar naƙuda suka yi mini. Haka kurum ruwan da suka sanya mini a hannuna ma na naƙuda ne.

Jin Hajiya Kilishi ta kama ni yasa na dawo hankalina izuwa kallonta, sannu ta dinga ce mini haka ma duk waɗanda ke wajen. Amma Aunty Salwa sai ma sabon kuka da ta saka ana ba ta haƙuri. Mamee kuwa ko motsi ba ta yi ba daga inda take zaune.

Bayan Hajiya Kilishi ta taimaka mini na yi wanka da ruwa mai zafin gaske, wanda ta cika bahon wanka, ta ce in shiga. Bayan na shiga ita kuma ta zuba wani a wata tasa mai faɗin gaske (silba), ta dinga tsoma tawul a ciki tana gasa mini jikina. Ni kuwa kamar kada ta daina saboda daɗin da nake ji.

Ina fitowa aka ba ni kunnun goruba cike da ƙwano aka ce in shanye shi. Ban ƙi sha ba, amma ni na san ba zan iya shanye shi ba. Lallai dole na yi mamakin har yanzu a ce Yarima bai shigo ya gan ni ba. Shin ko dai tsorona yake ji? Ko kuwa ya daina sona yanzu?

Kasa ɗaurewa na yi da na kalli agogon bango na ga har baƙwai da rabi na safe ta wuce, amma Yarima ba wanda bai shigo ya yi mini sannu ba, har da Dad ɗina da

yake nuna kawaici a kaina, sun shigo da shi da Mai Martaba Sarki. Ni dai kasa ɗaurewa na yi har na tambayi Hajiya Kilishi.

"Hajiya ina Yarima ne? Ko ya yi tafiya?"

"A'a yana nan, amma na ji Mai Martaba Sarki na cewa jikin nasa da sauƙi, yanzu haka suna wajen shi."

Hankalina na ji ya tashi matuƙa, da a ƙwance nake, amma sai gani na tashi zaune. Ya zan yi ni yanzu? Na tambayi zuciyata. Sai kawai na ji na miƙe tsaye. Hajiya ta yi saurin kama ni.

"Me ye?"

"Hajiya zan iya zuwa wajen Yarima?"

Eh,mu ma yanzu can zamu. Su Mamee ma na can tun ɗazu. Amma ganina da kinyi haƙuri sai Sarki ya tafi da mutanen shi,ki ƙwantar da hankalinki, ba abin da ya same shi, razana ce kawai ya yi."

#####

[3/1, 22:22] Ummi Tandama😇: *ƘASAITA BOOK 3*

NA

MARYAM KABIR MASHI

Ya ya zanyi? Dole na bi maganar manyana. Haka dole na koma na ƙwanta, amma hankalina duk baya jikina. Gudun kada a ce mini Yariman ya mutu, amma kaɗan-kaɗan na tambayi duk wanda na ga ya shigo, cewa, "Ina Yarima?" Sai dai su bani amsa da yana nan lafiya.

Ƙarfe biyu saura minti goma sha ɗaya na ga Yarima ya shigo cikin sauri. Yana shigowa ina ƙwance, ganinsa yasa na yi saurin tashi tsaye. Ya iso ya kama cinyoyin hannuwana duk biyun, ya zame hannayensa suka sauko ga ƴan yatsuna. Ya dawo da hannayensa ya shafi wuyana da su, ya tallabe kumatuna ya kalleni. Sai a lokacin na ga ya yi murmushi, ya mayar da ni ya rungume gam a jikinsa, ya ɗagoni ya zaunar da ni a bakin gado, shi kuwa ya tsugunna a gabana, da gani ya rasa ya zai yi mini. Sai na ga yasa ɗan yatsana a bakinsa.

A tunanina wasa zai yi mini,sai kawai ya cije ni, na sa ƙara irin wacce ke dawo da hankalin Yarima a gareni, sai kawai na ga yasa dariya. Nima ban san lokacin da nasa tawa dariyar ba. Sai na ga ya hayo gadon shi ma yana mai cigaba da dariya, ya mayar da ni ya rungume a jikinsa. Sai kawai na ji lema na tsiyaya cikin rigata ta bayana, na ɗago kansa.

"Yarima me ye kuma na fitar da hawaye bayan ga ni?"

"Yasmin da kin mutu da ya zanyi da ra....."

"Haba Yarima, kamar ba Musulmi ba,za ka dinga kawowa kanka irin wannan tunanin, ba ka san Allah mai rahama mai jin ƙai ne ba. Yanda Allah ya ɗauke maka ni, haka zai musanya maka da wacce ta fi ni."

"Ki yi shiru Yasmin,ke dai kawai ki taimaka mini da murna, da addu'ar godiya ga Allah da ya bar mini ke."

Hawaye ya tsiyayo a kumatunsa. "Ba zan taɓa iya ƙwatanta miki yanda na ji rayuwata ta koma ba a cikin ƙanƙanin lokaci."

"To ba sai..."

Jakadiya ce ta yi sallama, muka saki juna, sannan na ce ta shigo. Ta shigo tana rawar jiki da yaro rungume a hannunta. Har a lokacin ban fahimci me ta shigo yi ba, sai da ta durƙusa gabanmu tare da gaisuwar ta ta miƙo mini yaron hannunta. Sannan na tuna ashe fa haihuwa na yi,ni na ma yi tunanin abin da na haifa ya mutu, shi yasa ban ma neme shi ba.

Yarima ya miƙa hannu ya karɓa, ya ce da jakadiya, "Su Mai Martaba suna nan?"

Ta amsa da, "Suna fada,su Mama ne dai suka tafi."

Ya miƙo mini jaririn hannunsa ya miƙe.

"Tsaya ki kula da ita,in je in dawo"

Jakadiya ta ce, "To." Shi kuma ya sunkuyo ya sumbaci goshina sannan ya tafi.

Sai da na ga fitarsa sannan na dawo da kallona ga abin da ke hannuna, "Mace ce ko namiji?" Na tambayi jakadiya.

Ta amsa da "Namiji ne."

"Ina Suhailat?"

"Mama ta tafi da su ita da Ammar."

"Me yasa ba su zo yi mini sallama ba?"

"Saboda Yarima. Kai Gimbiya ki godewa Allah, Allah Yarima yana son ki,sumansa biyar da aka ce masa kin mutu. Ki duba taurin rai irin na Allah ya ja da rai, amma sai ga shi yana kuka a gaban kowa."

Na yi murmushi irin na wanda ya tashi daga ciwo, sannan na lalubi mama na sawa jariri a baki. Sai da ya kama maman, sannan na samu damar kallonsa sosai, abin ka da jariri sai na kasa gane da wa ya yi kama. Ina cikin ƙoƙarin gano hakan Aunty Salwa ta shigo.

**** **** ****

Rana ta zagayo aka sawa yaro suna Abdul Nasir,amma ba a yi wani taro ba, saboda jikina ya ƙara warwarewa, saboda haka Mai Martaba Sarki ya ce a barshi sai wani satin. Wannan yasa aka ƙara sa masu kulawa da ni su matso kusa da ni domin kulawa da ni sosai.

Su Ammar kuwa sun zama yan gidan Mama, saboda sai dai su zo da yawo su koma.

Bayan ƙwana uku da raɗin suna sai aka shigo falo na uku wanda nake zama domin hutawa, aka ce na yi baƙi. Ban tsaya neman ba'asi ba na ce su shigo. Sauran kaɗan in saki Abdul-Nasir ƙasa, saboda mamakin ganin baƙin su huɗu da na yi. Maza biyu, mata biyu,ba zancen koƙwanto na gane su, duk da sun canja kamaninsu. Cikin al'ajabi na kira sunan ɗaya daga cikin su.

"Mansura! Daga ina ku ke haka?"

Madadin su yi magana, sai kawai na ga Mansura tasa kuka, yɗar'uwarta Musulum na taya ta ko kuwa in ce suna taya juna.

"Su waye waɗannan?" Na tambaye su.

"Mazanmu ne, wannan mijin Mansura, wannan kuwa nawa."

"Daga ina ku ke haka? Ya aka yi ku ka san muna nan? Wa ya nuna muku gidan?"

"Mu ma labari muka samu, shi ne muka ce bari mu zo. Yanzu kuma muna ƙauyen Fembeguwa a zaune, saboda tsoron zama cikin birni gudun kada a sa a kamo mu."

Na kalli wacce ke kusa da ni, "A tafi da su wajen Sarkin gida ki ce baƙina ne a basu ɗakuna biyu, kowacce da mijinta. Ke kuma ki sa a basu komai da komai,ki tabbatar sun ci abinci."

Na juya ga su Mansura, "Ku je a baku masauki zan neme ku in kun huta."

"Mun gode. Amma za mu koma mu ɗauko yaranmu."

"Kun haihu ne?*

"Eh, yaranmu bibbiyu."

"To shi kenan, amma da mazan nan naku su je su ɗauko su."

"To Gimbiya, haka za'ayi." In ji mazan.

Daga nan suka miƙe,. Har sun kai ƙofa na kira Sa'a.

"Ki ce wani ya kai su su ƙwaso har kayansu."

"Tanko direba ko Brown?"

"Duk wanda aka samu."

Suka juya suka tafi suna ta godiya.

**** *** ****

Yau garin Jos ya ruɗe saboda hidimomin bakukuwa ga taron sunana da nake yi, wanda gaba ɗaya taron gidan mu ake yin sa. Duk girman gida irin namu, wanda zai kai kilo mita uku, amma cike yake da mutane. Get uku ne a ƙofar shiga, kenan wacce ke kallon kudu a kowanne zagayen get gidaje goma ne na fadawa.

Get ɗin farko yaran gida ke zaune a cikinsa, kenan masu yi mana hidimomi da yi wa dawaki, fulawoyi. Kai aikin gidan gaba ɗaya. Get na biyu kuwa yayan dogarawa, wasu daga cikinsu, wanda shi ma gida goma ne. Get na uku ne ke da gida ashirin na dogarawa.

Idan an shiga daga ɓangaren gabas,ƙaton falo ne ƙwaya ɗaya, sai ɗaki ɗaya ƙaton gaske,an yi shi ne domin saukar Mai Martaba Sarki na ɗaya, sai ɓangaren yamma kuma barandun sama ne aka yi guda huɗu. Kenan kowanne ɓangare da aƙwai baranda sai ƙaton fili daga tsakiya,an tanade shi ne saboda wani gagarumin taro kamar na yau. Filin dai kamar filin wasan ƙwallon ƙafa (Football).

Ɓangaren Arewa ƙaton masallaci ne a cikin shi,aƙwai Islamiyyar yara da ta manya, wanda mata su yi da safe, da yamma maza su yi da daddare. A nesa da masallaci

aka yi gidaje biyar. Limamin masallacin ke da ɗaya, ragowar huɗun malaman Islamiyya kowanne da matarsa da yaɗansa.

Idan aka iso ƙofar shiga gidan daga yamma kaɗan,ƙaton asibiti ne mai ƙunshe da ɗakuna taƙwas na jama'a kenan, sai ɓangaren manya aka yi wa likitoci hudu kacal. Dukkan gidajen ɗakuna biyu ne da falo a cikin shi, sai kuwa ɗakin samari a bayan gida, wanda yake tare da banɗakinsa.

Manyan falo taƙwas ne a gidan, uku na shi, uku nawa, dukkansu na karbar baƙi ne, amma ƙofa biyu ce ta shiga gidan da ƙofar shiga falona, sannan da ta shiga nashi falon.

Ɗaya cikin ɗaya ne, sai in da muke son zama. Ganin baƙin idan aka fita daga falukan namu da aƙwai wani fili a tsakiyar falukan, wanda ya ƙunshi ƙofofi biyu. Ɗaya ta shiga falon sa, koma in ce sashen shi, ɗaya kuwa ta shiga nawa sashen, amma idan ka shiga falo ne kowa a farko shine falukan mu mu da yaranmu. Kenan personal falon mu,amma kuma daga cikin falon kowa zaka iya shiga na ɗaya, kenan haɗe muke waje ɗaya, sai dai kowa da ɓangarensa.

Ɓangarena ɗakuna baƙwai ne, amma ɗaya ne nawa, sai na yara ɗaya, na ƙwamfuta ɗaya. Haka nan yake ba kowa a ciki,an yi shi ne kawai saboda baƙin a na kusa. Biyu kuwa na masu kula da ni da gidana da yayana, wanda su nasu kamar an yi su ne daga gefe ɗaya tare da banɗakinsu har da yar barandar su ta shan iska.

Nasa ɓangaren ɗakuna biyu ne kacal, ɗaya nasa, ɗaya na ƙwamfuta (Computer). Tsayawa lissafa abin da ke cikin gidan ma asarar baki ne, saboda ya dame gidanmu na farko sau ba iyaka. Idan kuwa an fita daga cikin ƙofar shigowar kuwa,nan kicin yake da sito, kenan ƙofar shigowa falona na cikin gida, amma na taryar baƙi, saboda ni biyu kenan cikin gida, ɗaya kuwa na cikin gida na karɓar baƙi, ɗaya yan gida ko mabuƙata.

In an zagaya bayan gida, barga ce, kenan ɗakuna ɗai ɗaya da banɗaki a jere guda taƙwas na ma'aikata ne masu yin abinci mata, da kicin ɗin su ƙaton gaske na yin abincin yan barga da duk wani baƙon da zai yi sallama, da wajen ajiye ajiyensu na kayan abinci.

Gefensu daga ɗan nesa kaɗan gidaje ne uku a kulle,su ma ɗaki biyu da falo ne, bayan gida duka kuwa ƙaton lambu ne cike da kayan marmari, waɗanda ba rani ba damina, duk kullum da yayan a jikinsu, amma tsakiyar lambun ruwa ne ke gudu ta ko'ina ka waiga za ka ga duwatsu, ballantana ma cikin lambun.

Yau ne aka ɗaurawa Ahmad aure shi da Idris ƙannan Yarima kenan, waɗanda suka auro yayan daga wajen garin nan. Ahmad ɗiyar Daraktan (Director) ce a Katsina, wanda suka haɗu da yarinyar a ƙasar Spain,inda ya yi karatunsa, wanda ita ma karatun ya kai ta. Duk da ita ba ta gama ba, saura shekara biyu, wannan yasa ma in an gama bikin can za su koma da zama har sai ta kammala, shi kuma zai yi wani karatun tattalin arzikin ƙasa a matsayin digirinsa na biyu.

Shi kuwa Idris ɗiyar Sarkin Dutse ce ta jihar Jigawa. Yara ƙyawawa, Fulanin asali yayan Sarkin adalci na ƙasa. Ana cikin hidimar biki ne na ga Mabaruka, muka gaisa. A nan ta ke bani labarin ta yi aure har ta haifi ɗan ta namiji yana gida ta baro shi. Nan ta yi mini barka da arziƙi.

**** *** ****

"Kai na gaji!”

Na ce daidai lokacin da na ƙwanta cinyar Yarima, wanda ke lallaɓa Nasir ya yi bacci. Ya waiga ya ja kunnena wai faɗan zan tashi Nasir. Na yi ƙara, haka kuwa ya sa ya tashi, da guduna na ruga saboda na san Honey zai iya cizona a kumatuna ko ma na sha mintsini.

Ya cije leɓe, "Zan rama ne."

Na yi masa gwalo. Ya ɗauko Abdul Nasir ya biyoni a guje. Abin ka da ƙaton ɗaki, sai na dinga zagaye a ciki. Kafin ya kamo ni jakadiya ta yi sallama. Na tsaya tare da kallon agogo. Ƙarfe sha ɗaya na dare,me jakadiya ta zo yi yanzu ɗakin mijina?.

Kafin in gama tunani Yarima har ya bata izinin shigowa. Tana shigowa ta yi saurin zama ƙasa.

"Allah ya ja da rai an iso da ita, tana ɗakinta.”

Ya yi shiru ta kai minti uku, sannan na ji ya yi magana.

"Ki ce ina yi masu sannu da zuwa. Bayan minti ashirin ki kawo ta nan ta gaishe da Yayarta,su san juna."

Na yi tsaye, amma ban fahimci komai ba, har jakadiya ta gama kirarinta ta tafi.

Inda na ke tsaye ya iso yana dariya, ya kama ni, "Na kama ta! Na kama ta!! Nasir mai za mu yi mata?"

Yasa hannu ya mintsini kunci na ɗaya.

"Tsaya don Allah Yarima,wai wacece aka kawo? Ban fahimci maganar ku ba?”

"Za ki gan ta yanzu.”

"Wace ce?"

######

[3/2, 15:46] Ummi Tandama😇: *ƘASAITA BOOK 3*

NA

MARYAM KABIR MASHI

"Amaryar ki. Ko kin manta ne?"

Na ɗauki hannunsa mai shafa kumatuna na ajiye gefe. Na karɓi ɗana daga hannun shi, na tafi na zauna bakin gado. Tun da na ƙurawa ƙasa ido ban kuma ɗagowa ba. Magana ba irin wacce Yarima bai yi mini ba, ballantana in kalleshi. Babu abin da Yarima bai yi mini ba, amma ko motsi ban yi ba. Har cakulkuli ya yi mini,amma motsi na kasa yi, alhali abin da ke sani ƙarar wasa da ihun neman ceto,idan Yarima na yi mini shi.

Ganin na zama mutum-mutumi yasa ya ƙyale ni ya koma saman kujera ya ƙwanta yana ta ƴan surutai.

"Ni ki ka ƙyale? Mijinki ne fa, shi kenan na gode."

Ya samu ɗan tsayin lokaci, sannan na ji sallamar mata. Inda na ke zaune na ji gabana ya faɗi.

"Ku shigo jakadiya."

Jakadiya na gaba ragowar na biye da ita har gaban wanda ya basu iznin shigowa ɗakin.

"Barka da dare?"

Haka na ji an ce cikin siririyar murya.

"Barka da zuwa amarya."

Jin an zauna kusa da ni yasa hankalina ya dawo dai-dai.

"Yasmin." Na ji an ambaci sunana. Ban iya amsawa ba. Bai jira na amsa ba ya ci gaba.

"Wannan ita ce ƙanwar ki Asabe, daga yau kin zama babba a gidan nan, saboda haka ki riƙe girman ki."

Ya juya ga Asabe ya ce, "Asabe."

"Na'am, Sarkin Sarakuna."

A take na ji wasu abubuwa guda uku sun tsaya a ƙirjina.

"Wannan ita ce Yayarki,kin gan ta, aure ne tsakanina da ita, ina son ta matuƙa, ita ce sirrin zuciyata, ita ce ƘASAITAR jikina, saboda haka kiyi biyayya a gare ta,idan kuwa na samu akasin haka, zan saɓa miki matuƙa."

"Yasmin ga Asabe.”

Na ƙi motsawa.

"Asabe ga Yayarki Gimbiya Yasmin.”

"Allah ya ja da ran Gimbiya Yayata.”

Na ji an dafa mini yɗan yatsun ƙafa ta.

Wannan ya ba ni damar matse jaririna a jikina, har yasa ihu.

"Yasmin,kawo shi. Ke sakar shi kin matse shi da yawa. Jakadiya ku tafi gani nan zuwa."

Ina jin fitar su jakadiya, sai na ji abubuwan nan uku sun danne mini ƙirji,da ƙyar lumfashina ke fita.

Ina jin shi yasha kokawar ƙwaƙule Abdul-Nasir da ke ƙwalla kuka, amma na hana. Ina ji ya hayo gado sosai, ya bi bayana. A daidai kunnena na ji yana magana, tare da zuge zub ɗin rigar baccina.

"My love, kada ki sa zuciyata ta fashe mana,ki yi tunanin alƙawarin da ki ka ɗauka a Kaduna, wannan alƙawari sai da na nanata shi a gaban Sarki, saboda hotunan da aka kai masa da kaset, na san ba ki san ko waɗanne ba ne. Waɗanda ki kasa aka yi a mota lokacin da ki ka tsare ni, lokacin da ki ka sa aka kai ni a hotel na yi ƙwana uku ban ga ƙyakƙyawar fuskar ki ba."

Ya saɓule rigar jikina yasa hannunsa ta bayana ya rungume ni.

"Yasmin ba zan iya son kowacce mace ba sai ke. Please ba ni Abdul ki tuna wahalar da muka sha kafin mu same shi.”

Lallashin yasa na miƙa masa Nasir,sai na ji yana ta lallashin shi, amma ya ƙi yin shiru. Ya zagayo ya ɗora shi a cinyata ya zaro mama ya saka masa a baki. Yaro ya dinga sha, wannan yasa na saka kuka.

"Me ye na kuka Yasmin?"

"Ɗanka ne fa." Na cuci kaina dana tuno abin da na sa aka yi maka a hotel.

Haya na ɗauki wata karuwa, aka ba shi baliyan maganin bacci, ya sha, shi ne ta cire masa riga, ita ma ta cire ta ƙwanta a ƙirjinsa, shi ne nasa aka ɗauke su hoto. Haka sai kuma muka haɗa kai da ita a kan ta san yanda aka yi aka haɗa wannan kaset ɗin. Haushi takaici suka tarar mini.

Ya tsugunno gabana, "Honey zan tafi" na yi shiru.

"Ba za ki yi mini addu'ar dawo lafiya ba?"

Wani ƙwarin gwiwa ya zo mini da na tuna abin da Aunty Salwa take gaya mini a kan idan namiji na son abu,ka nuna ka fi shi so, haushi ma ka ke bashi.

"Na ji kin yi shiru?"

"Yanzu zan yi magana ka riga ni. A dawo lafiya, a gaishe da amarya.”

"A'a, sai dai ki zo mu je ki raka ni.”

"Ba damuwa, jira ni Abdul Nasir, ya kammala sai na raka ka. Ka sa manyan kaya mana."

"A'a waɗannan ma sun isa,gudun kada ta sha wahala wajen tuɓe mini."

Na harare shi kaɗan, "Ni tashi mu tafi."

"Ba komai in na je zan gaya mata,in ce harara ta ma ki ka yi. Amma bayan kin gama kuka."

"Ni ba kai nayi wa kuka ba, kaina na yi wa kuka. Ka ga a daina wannan maganar, tashi mu je. Amma gaskiya sai an gyara ka."

Na miƙe na ajiye Nasir,na isa na ɗauko wata sabuwar doguwar rigar hutawa da alkyabba na iso gaban shi. Yana tsaye na cire kayan jikinshi na sa masa sababbi, ban da turare da na dinga fesa masa.

Ni ce har da farar hoda sai da na shafa masa, saboda ya ƙara fitowa. Kallon mamaki na ga yana yi mini. Na ɗauko takalma na durƙusa na ajiye masa. Ina ɗagowa zan juya ya riƙo hannuna, madadin ya yi magana, sai kawai na ga ya haɗa ni da jikinsa, haɗa kumatuna ya yi duk biyun ya ɗago su sama, sai kawai na ga ya haɗa bakina da nasa yana tsotsa kamar zai mayar da ni ciki. Har wani jikinshi ke rawa.

Na ɗago kansa, "Lafiya Yarima?" Bai iya amsa mini ba. Zame jikina daga gare shi na yi, na tafi cire rigar baccin jikina, ina faɗar.

"A yi rakiyar ango da rigar bacci?" Sai da na tabbatar ni yake kallo, sannan na saki rigar baccin ƙasa, daga ni sai ɗan wando, sai kuwa rigar mama, sannan na ɗauko kaya na fara sakawa.

Jin an riƙe mini hannuwa, waɗanda ke ƙulle zanena ta baya, shi yasa na ɗan yi alamar na tsorata.

"Au! Da kai ne har ka bani tsoro?" Na juya zan cigaba, ya riƙe ni.

"Yasmin kin daina sona ne?"

"Me ka gani?"

"Ga ni nayi murna ki ke yi zan tafi in barki."

"Ba haka ba ne ba,dama ai yanzu dole ne so ya ragu, tun da mun zama mu biyu, balle ita fa ganinta ka yi ka ce kana son ta. Ni kuwa fa,ƙyauta ta aka yi....."

Ya zagayo gabana tare da nuna hankalinsa ya tashi, ya riƙe kafaɗuna ya zame hannayena da ganin yanda yake yi ya rasa yanda zai yi, ya ɗauko rigar da alkyabba ya miƙo mini.

"Sa ka zo mu tafi. Ya juya ya ɗauki Nasir,ni kuwa a hankali na saka kayana, ganin na cika nawa, ya zo ya kama hannuna, hannu ɗaya na tallabe da Nasir.

Kusan in ce ja na ya dinga yi ba ma tafiya ba da sauri. Bai zame ko ina ba sai ɗakin jakadiya, wanda yake sashen gidana.

"Jakadiya." Kiran da ya yi mata kenan. Ta fito da sauri tare da kifawa ƙasa da sauri.

"Ga ni Allah ya huci zuciya, daidai nake da a hukunta ni idan har an same ni da laifi."

"Mansura! Ina Mansura?"

"Tana ciki?"

"Kira ta.”

Ta miƙe da saurinta ta shiga wani ɗaki,a inda na ga ta shigo da amaryar da aka kai min ɗakina. A tsaye na yi wa kaina tagwayen tambayoyi. "Shin Mansura ya aura? Ina mijinta? Amanata suka ci ko me? Ai kuwa...."

"Jakadiya ya aka yi?"

"Allah ya ja da ran Gimbiya,dama haɗa baki muka yi da Mai Martaba Yarima, ya ce a rufawa Mansura kaya a kai masa ita domin a zolaye ki, saboda ya zamo jan kunne a gare ki na ƙin daina yiwa mijinki alƙawarin kin amincewa ya yi aure.”

"To kin ganta nan, nuna mini ta yi bata sona yanzu don na yi haka."

Na san halin Yarima a kaina, wannan yasa na yi yɗar dabarar dariya ni kuma irin ta mu ta manya.

"Jakadiya, nunawa ya yi ni yanzu an gama da ni. Ni kuwa na nuna masa ni kuma yanzu nake yayin kaina, shi ne ya ji haushi.”

Ya ɗago hannu zai ɗan kai mini duka, na goce. Aka sa dariya, shi ma sai na ga ya yi dariya.

"Jakadiya haɗe mini kai ku ka yi da Gimbiyar taki. Zan rama, sai na yi maku bazata.”

Muka yi dariya, sannan ya juya.

"Sai da safen ku, ga angon ki nan na kawo muku har da ribar ɗa."

"Wallahi." Ya faɗa. Ni kuwa na juya. Bai shigo ba sai da har na ƙwanta. Yana shigowa ya wuce gadon Nasir ya ƙwantar da shi, sannan ya zo ya zauna gefen gado.

"Yasmin."

"Ina jin ka."

"Taso nan." Na mirgino na sauka na tsugunna gabansa.

"Matso." Na matsa.

"Ɗago." Na ɗago. Yanda yake tamkar an yi durƙushen raƙumi, kunnena ya kama har da, yar ƙara na yi masa.

"Daga yau kada in ƙara jin kin ce ai ba ni ne na gan ki na ce ina son ki ba. Kina jina?"

Na ɗaga kaina.

"Kada kuma ki ƙara cewa wai kin daina sona,in na ƙara jin haka, duk hukuncin da na yi miki ke ki ka ja. Yanzu ma don ina tausaya miki sati biyu da suka wuce kin sha wahala da yawa, da sai na kai ki ƙara wajen Daddy ya yi mana Shari'a."

"Na tuba,saboda Daddy na yanzu ya fi sonka da ni. Kada kasa ya zane ni da bulala."

"Honey,an ruɗe an ga amarya."

"Dole in ruɗe. Ka yi tunanin yanda ka ke nuna mini so,ƙauna a gaban kowa,yau in wayi gari in ga ana yiwa wata irin shi. Ka san yau da da gaske ne,ƙila in ƙarasa mutuwar da na kusan yi rana....."

"Kada ki tayar mini da hankali. Yanzu a bar wannan maganar." Ya ɗago ni ya zaunar da ni a cinyarsa.

"Ni yanzu tunanin da nake shi ne me zan yi wa Jakadiya da su Mansura?" Na yi ɗan shiru kaɗan.

"Honey akan me?"

"Na ɓangaren ƙyauta."

"Eh, gaskiya, amma ni na san Jakadiya ba za ta bar gidan nan ba, da zata iya barin shi da sai a bata ƙyautar gida cikin gari ta koma ita da yayanta da jikokinta."

"To tun da kin yi wannan tunanin,to ko mu samu gida mu saya mai ƙyau babba a baiwa yayanta su tashi daga gidan sarauta a basu jari. Ita kuma a ɗebi bayan gida a yi mata gidanta mai ƙyau a zuba mata komai."

"Haka za'ayi Mai Martaba na biyu. Su Mansura kuwa na san har ka gama tunanin yanda za ka yi dasu. Abin da ya rage ni,ni kuma ina son zuwa gidan Yaya Ahmad a can Spain in ɗan huta,ka ga har na gaido kakannina,in gano iyalinshi ma."

"Ki bar wa?"

"In bar ka, ka san Sarki ba yawo,wa zaka barwa mulkin?"

"Ki yi shiru ko in gama ki da Mama."

"Gaskiya ni....”

Sai kawai na ga ya ɗauki waya. Na yi saurin alamar ƙwacewa, ya haye gado. Na bi shi sai na ji yana cewa.

"Barka da dare Mama.... lafiya ƙalau.... ga ta nan dama ita ce take...”

"Barka da dare Mama."

"Lafiyar shi lau, ga shi can yana bacci."

"A'a dama cewa na yi bari in shigo mu gaisa."

"To, to, insha Allah sai anjima.”

"Mama,Mama.” na yi saurin rufe bakinsa.

"Na tuba na haƙura."

"Kin rufawa kanki asiri da yanzu kin sa na koma ƘASAITA ta in dinga ja miki rai.”

"Me ka ce?"

"Cewa na yi ƙASAITA,a waje ake yin ta ba a gida ba wajen iyali. A gida Honey ita ke da ƘASAITA. Ni kuwa sai in zama shalelenta."

Yanzu kuma sai dai in yi miki godiya game da shawarwari da haɗin kai da ki ka ba ni har na zamo na samu ɗaukaka ga jama'a da mahaifina, ga talakawa, yanzu komai ya wadace su ba sai na tsaya jiran gwamna ko shugaban ƙasa ba. Na gode da shawarwarin ki.”

"Tsaya ina da magana."

Ina jin ki."

"Amma na gama haihuwa haka nan?"

"Ki ɗan ƙara ɗaya."

"Ni dai a'a." Yana dariya wai ganin yanda na yi. Ya rungume ni.

"My love,my life,my body,my soul. Na gode Allah da ya ba ni ke."

Ya janyo ni muka ƙwanta tare da kashe fitilar ɗakinmu. Addu'ar ƙwanciyar bacci ita ta zamo murfin maganarmu, sai dai muka yi wa junanmu addu'a a zuciya, ta Allah ya taya mu riƙon junanmu.

ALHAMDULILLAH!

Na gode

Mai ƙaunarku a kullum:-

AUNTY MARYAM KABIR MASHI.